# Suratul Mulk

An Saukar Da Ita A Makkah



سُورَةُ المُلْكِ
آياتها ٣٠ ترتيبها ٦٧

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

الجزء ٢٩ الحزب ٥٧ تَبَٰرَكَ ٱلَّذِي بِيَدِهِ ٱلۡمُلۡكُ وَهُوَ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ قَدِيرٌ ١ ٱلَّذِي خَلَقَ
ٱلۡمَوۡتَ وَٱلۡحَيَوٰةَ لِيَبۡلُوَكُمۡ أَيُّكُمۡ أَحۡسَنُ عَمَلٗاۚ وَهُوَ ٱلۡعَزِيزُ ٱلۡغَفُورُ
٢ ٱلَّذِي خَلَقَ سَبۡعَ سَمَٰوَٰتٖ طِبَاقٗاۖ مَّا تَرَىٰ فِي خَلۡقِ ٱلرَّحۡمَٰنِ مِن
تَفَٰوُتٖۖ فَٱرۡجِعِ ٱلۡبَصَرَ هَلۡ تَرَىٰ مِن فُطُورٖ ٣ ثُمَّ ٱرۡجِعِ ٱلۡبَصَرَ كَرَّتَيۡنِ
يَنقَلِبۡ إِلَيۡكَ ٱلۡبَصَرُ خَاسِئٗا وَهُوَ حَسِيرٞ ٤ وَلَقَدۡ زَيَّنَّا ٱلسَّمَآءَ
ٱلدُّنۡيَا بِمَصَٰبِيحَ وَجَعَلۡنَٰهَا رُجُومٗا لِّلشَّيَٰطِينِۖ وَأَعۡتَدۡنَا لَهُمۡ عَذَابَ
ٱلسَّعِيرِ ٥ وَلِلَّذِينَ كَفَرُواْ بِرَبِّهِمۡ عَذَابُ جَهَنَّمَۖ وَبِئۡسَ ٱلۡمَصِيرُ
٦ إِذَآ أُلۡقُواْ فِيهَا سَمِعُواْ لَهَا شَهِيقٗا وَهِيَ تَفُورُ ٧ تَكَادُ تَمَيَّزُ
مِنَ ٱلۡغَيۡظِۖ كُلَّمَآ أُلۡقِيَ فِيهَا فَوۡجٞ سَأَلَهُمۡ خَزَنَتُهَآ أَلَمۡ يَأۡتِكُمۡ نَذِيرٞ ٨
قَالُواْ بَلَىٰ قَدۡ جَآءَنَا نَذِيرٞ فَكَذَّبۡنَا وَقُلۡنَا مَا نَزَّلَ ٱللَّهُ مِن شَيۡءٍ إِنۡ أَنتُمۡ
إِلَّا فِي ضَلَٰلٖ كَبِيرٖ ٩ وَقَالُواْ لَوۡ كُنَّا نَسۡمَعُ أَوۡ نَعۡقِلُ مَا كُنَّا فِيٓ أَصۡحَٰبِ
ٱلسَّعِيرِ ١٠ فَٱعۡتَرَفُواْ بِذَنۢبِهِمۡ فَسُحۡقٗا لِّأَصۡحَٰبِ ٱلسَّعِيرِ ١١ إِنَّ
ٱلَّذِينَ يَخۡشَوۡنَ رَبَّهُم بِٱلۡغَيۡبِ لَهُم مَّغۡفِرَةٞ وَأَجۡرٞ كَبِيرٞ ١٢



## Daga Manufofin Surar:

**Bayyana cikar mulkin Allah da ikonsa, domin a ji tsoronsa, kuma a guji uqubarsa.**

## Tafsir:

**(1) Alherin Allah, wanda mulki yake hannunsa shi kaxai ya yawaita kuma ya girmama, kuma shi mai iko ne a kan komai, babu abin da yake gagararsa. (2) Wanda ya halicci mutuwa, kuma ya halicci rayuwa, domin ya jarraba ku - Ya ku mutane - wanene a cikinku ya fi kyautata aiki, Shi ne Mabuwayi wanda babu mai rinjayarsa, mai yawan gafara ga zunuban waxanda suka tuba daga cikin bayinsa. (3) Wanda ya halicci sammai guda bakwai, kowace sama tana rufe da ta qasa da ita, ba tare da suna gogar juna ba. Ya kai mai duba, ba zaka tava ganin rashin dacewa a cikin halittar Allah ba, ka daxa mayar da ganin ka shin zaka ga wata tsaga ko kecewa?!. Ba zaka ga haka ba, sai dai ka ga wata halitta mai kyau da qwarewa a cikinta. (4) Ka sake mayar da ganinka, karo bayan karo, ganinka zai dawo maka cikin qasqanci, ba tare da ya ga wani aibu ba a cikin halittar sama, kuma haka ganinka zai dawo yana gajiyayye, ba tare da ya ga komai ba.**

**(5) Tabbas mun qawata saman da ta fi kusa da qasa, ta hanyar sanya mata taurari masu haske, kuma muka sanya waxannan taurari suka zama masu xauke da wuta, ana jifar Shaixanu masu satar ji da su, sai su qone su, kuma a lahira mun tanadar musu wuta mai ruruwa. (6) Waxanda suka kafirce wa Ubangijinsu a ranar alqiyama suna da azaba ta wuta wadda aka rurata, kuma makomarsu wadda zasu koma cikinta ta yi muni.**

**(7) Idan aka wurga su a cikin wutar, sai su ji wani sauti mai tsananin muni, kuma tana tafasa kamar yadda tukunya take tafasa. (8) Sashenta ya kusa ya rabe da sashe, ya bambanta da shi, saboda tsananin fushinta a kan duk wanda ya shige ta. Duk lokacin da aka jefa wasu jama'a daga ma'abotanta daga cikin kafirai, sai Mala'ikun da wakilta su kula da ita su tambaye su, tambaya da tsoratarwa, su ce: "Yanzu Manzo bai zo muku a duniya, yana tsoratar da ku azabar Allah ba?!. (9) Sai Kafirai su ce: "Haka ne, tabbas Manzo ya zo mana, yana tsoratar da mu azabar Allah, amma sai muka qaryata shi, muka ce msa: "Babu wani wahayi da Allah ya saukar, ku Manzanni ba kwa kan komai sai vata mai girma daga barin gaskiya".**

**(10) Kafirai suka ce: "Da a ce mun kasance muna ji, jin da ake amfana da shi, ko muna hankalta, hankalin da ake bambance gaskiya da qarya da shi, da bamu kasance cikin 'yan wuta ba, da mun yi imani da Manzanni, mun gasgata abin da suka zo da shi, mun kasance cikin 'yan Aljannah.**

**(11) Sai suka tabbatar da kafirci ga kansu, da kuma qaryata Manzanni, don haka sai suka cancanci shiga wuta, tir da ma'abota wuta.**

**Yayin da Allah ya ambaci siffofin kafirai da sakamakonsu, sai ya biyo baya da ambaton siffofin masu imani da sakamakonsu, ya ce:**

**(12) Haqiqa waxanda suke jin tsoron Allah yayin da suka kaxaita, suna da gafarar zunubansu, kuma suna da lada mai girma, shi ne Aljannah.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - A cikin sanin hikimar halittar mutuwa da rayuwa akwai abin da yake wajabta gaggawa zuwa aiki nagari kafin mutuwa. 2 - Fusatar wutar Jahannama a kan kafirai, kishi ne ga Allah (S.W.T). 3 - Aljanu sun riga mutane zuwa sararin samaniya, amma duk wanda ya qetare iyakarsa daga cikinsu to zai gamu da uqubar da take jiransa. 4 - Yin xa'a ga Allah, da jin tsoronsa a voye yana janyo gafarar Allah, da shiga Aljannah.**

وَأَسِرُّواْ قَوۡلَكُمۡ أَوِ ٱجۡهَرُواْ بِهِۦٓۖ إِنَّهُۥ عَلِيمُۢ بِذَاتِ ٱلصُّدُورِ ١٣ أَلَا
يَعۡلَمُ مَنۡ خَلَقَ وَهُوَ ٱللَّطِيفُ ٱلۡخَبِيرُ ١٤ هُوَ ٱلَّذِي جَعَلَ لَكُمُ ٱلۡأَرۡضَ
ذَلُولٗا فَٱمۡشُواْ فِي مَنَاكِبِهَا وَكُلُواْ مِن رِّزۡقِهِۦۖ وَإِلَيۡهِ ٱلنُّشُورُ ١٥
ءَأَمِنتُم مَّن فِي ٱلسَّمَآءِ أَن يَخۡسِفَ بِكُمُ ٱلۡأَرۡضَ فَإِذَا هِيَ تَمُورُ ١٦
أَمۡ أَمِنتُم مَّن فِي ٱلسَّمَآءِ أَن يُرۡسِلَ عَلَيۡكُمۡ حَاصِبٗاۖ فَسَتَعۡلَمُونَ
كَيۡفَ نَذِيرِ ١٧ وَلَقَدۡ كَذَّبَ ٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِهِمۡ فَكَيۡفَ كَانَ نَكِيرِ ١٨
أَوَلَمۡ يَرَوۡاْ إِلَى ٱلطَّيۡرِ فَوۡقَهُمۡ صَٰٓفَّٰتٖ وَيَقۡبِضۡنَۚ مَا يُمۡسِكُهُنَّ إِلَّا
ٱلرَّحۡمَٰنُۚ إِنَّهُۥ بِكُلِّ شَيۡءِۭ بَصِيرٌ ١٩ أَمَّنۡ هَٰذَا ٱلَّذِي هُوَ جُندٞ لَّكُمۡ
يَنصُرُكُم مِّن دُونِ ٱلرَّحۡمَٰنِۚ إِنِ ٱلۡكَٰفِرُونَ إِلَّا فِي غُرُورٍ ٢٠ أَمَّنۡ هَٰذَا
ٱلَّذِي يَرۡزُقُكُمۡ إِنۡ أَمۡسَكَ رِزۡقَهُۥۚ بَل لَّجُّواْ فِي عُتُوّٖ وَنُفُورٍ ٢١ أَفَمَن
يَمۡشِي مُكِبًّا عَلَىٰ وَجۡهِهِۦٓ أَهۡدَىٰٓ أَمَّن يَمۡشِي سَوِيًّا عَلَىٰ صِرَٰطٖ
مُّسۡتَقِيمٖ ٢٢ قُلۡ هُوَ ٱلَّذِيٓ أَنشَأَكُمۡ وَجَعَلَ لَكُمُ ٱلسَّمۡعَ وَٱلۡأَبۡصَٰرَ
وَٱلۡأَفۡـِٔدَةَۚ قَلِيلٗا مَّا تَشۡكُرُونَ ٢٣ قُلۡ هُوَ ٱلَّذِي ذَرَأَكُمۡ فِي
ٱلۡأَرۡضِ وَإِلَيۡهِ تُحۡشَرُونَ ٢٤ وَيَقُولُونَ مَتَىٰ هَٰذَا ٱلۡوَعۡدُ إِن كُنتُمۡ
صَٰدِقِينَ ٢٥ قُلۡ إِنَّمَا ٱلۡعِلۡمُ عِندَ ٱللَّهِ وَإِنَّمَآ أَنَا۠ نَذِيرٞ مُّبِينٞ ٢٦



**(13) Ya ku mutane, ko ku voye maganganunku ko ku bayyana su, duk Allah ya sani, domin shi Allah masanin abin da yake cikin zukatan bayinsa ne, babu wani abu da yake vuya a gare shi.**

**(14) Yanzu wanda ya halicci halitta gaba xaya, a ce bai san sirri ba, da ma abin da ya fi sirri voyuwa ba?! Alhali shi ne mai tausasawa ga bayinsa, Masanin al'amuransu, babu abin da yake vuya a gare shi.**

**(15) Shi ne wanda ya sanya muku qasa ta zamo mai laushi a gare ku, don ku zauna a kanta, ku yi tafiya a sasanninta, ku ci daga arzikin da Allah ya tanadar muku a cikinta, shi kaxai ne zai tashe ku, don yin hisabi da bada sakamako.**

**(16) Shin kun amince Allah wanda yake sama ya keta qasa a qarqashinku, kamar yadda ya keta ta ga Qaruna, bayan ta kasance mai sauqi don zama a kanta, a wayi gari tana motsi da ku, bayan ta kasance a kafe?!.**

**(17) Ko kuwa kun amince Allah wanda yake sama, ya aiko muku da duwatsu daga cikin sama, kamar yadda ya aiko su ga mutanen Annabi Luxu?!. Da sannu zaku san gargaxina da uqubata a lokacin da zaku ga azabata, sai dai ba zai yi muku wani amfani ba, bayan kun ga azaba.**

**(18) Haqiqa Al'ummun da suka rigayi waxanan mushirikai sun qaryata, sai azabar Allah ta sauka a kansu, yayin da suka zarce a kan kafircinsu da qaryatawarsu, to kalli yaya inkari ya kasance a kansu?! Haqiqa inkarina ya kasance mai tsanani ne.**

**(19) Shin waxannan masu qaryatawa basu ga tsuntsu ba ne a samansu, suna yin sahu, wasu a gefen wasu, babu wanda yake riqe su don kada su faxo qasa sai Allah, domin shi mai gani ne ga komai, babu abin da yake vuya a gare shi.**

**(20) Ya ku Kafirai baku da wata runduna da zata kare ku daga azabar Allah, idan ya yi nufin ya azabtar da ku, kafirai yaudarar kansu kawai suke yi, shaixan ya yaudare su, sai suka ruxu da shi.**

**(21) Kuma babu wanda ya isa ya baku arziki idan Allah ya hana arziki ya isa gare ku, kawai dai kafirai sun ci gaba da kangarewa Allah da girman kai, da qin gaskiya.**

**(22) Yanzu wanda yake tafiya bisa fuskarsa a kife - Shi ne mushiriki – shi ne ya fi shiriya, ko kuwa mumini wanda yake tafiya daidai a kan tafarki madaidaici?!.**

**(23) Ya kai wannan Manzo, ka faxawa waxannan mushirikai masu qaryatawa: "Allah ne ya halicce ku, ya sanya muku kunnuwa, da kuke ji da su, da idanuwan da kuke gani da su, da zukata da kuke hankalta da su, sai dai kaxan ne kuke godewa Allah a kan ni'imomin da ya yi muku.**

**(24) Ya kai wannan Manzo, ka faxawa waxannan mushirikai, masu qaryatawa cewa: "Allah ne ya yaxa ku a bayan qasa, ya barbaza ku a kanta, ba wai gumakan ku ba ne, waxanda basa halittar komai, kuma ga Allah ne kaxai za a tara ku ranar alqiyama, domin yi muku hisabi da sakayya, ba zuwa gumakanku za a tara ku ba, don haka ku ji tsoron Allah shi kaxai, ku bauta masa shi kaxai.**

**(25) Masu qaryata tashin alqiyama, waxanda suke ganin ba zai yiwu ba, suna cewa,: "Yaushe ne wannan alqawari da kake ta yi mana - Ya kai Muhammad - kai da sahabbanka zai kasance, indai har da gaske ku ke yi na cewa zai zo?!.**

**(26) Ya kai wannan Manzo, ka ce musu: "Sanin lokacin tashin alqiyama yana wajen Allah, ba wanda ya san yaushe ne sai shi, ni kaxai mai gargaxi ne gare ku, gargaxi bayyananne.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa: 1 - Allah yana ganin abin da zukatan bayinsa suke voyewa. 2 - Kafirci da savon Allah suna cikin sabubban da suke kawo azabar Allah a duniya da lahira. 3 - Kafircewa Allah duhu ne da ruxu, imani da shi haske ne da shiriya.**

فَلَمَّا رَأَوۡهُ زُلۡفَةٗ سِيٓـَٔتۡ وُجُوهُ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ وَقِيلَ هَٰذَا ٱلَّذِي كُنتُم
بِهِۦ تَدَّعُونَ ٢٧ قُلۡ أَرَءَيۡتُمۡ إِنۡ أَهۡلَكَنِيَ ٱللَّهُ وَمَن مَّعِيَ أَوۡ رَحِمَنَا
فَمَن يُجِيرُ ٱلۡكَٰفِرِينَ مِنۡ عَذَابٍ أَلِيمٖ ٢٨ قُلۡ هُوَ ٱلرَّحۡمَٰنُ
ءَامَنَّا بِهِۦ وَعَلَيۡهِ تَوَكَّلۡنَاۖ فَسَتَعۡلَمُونَ مَنۡ هُوَ فِي ضَلَٰلٖ مُّبِينٖ
٢٩ قُلۡ أَرَءَيۡتُمۡ إِنۡ أَصۡبَحَ مَآؤُكُمۡ غَوۡرٗا فَمَن يَأۡتِيكُم بِمَآءٖ مَّعِينِۭ ٣٠

آياتها ٥٢ سُورَةُ القَلَمِ ترتيبها ٦٨

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

ربع الحزب ٥٧ نٓۚ وَٱلۡقَلَمِ وَمَا يَسۡطُرُونَ ١ مَآ أَنتَ بِنِعۡمَةِ رَبِّكَ بِمَجۡنُونٖ ٢ وَإِنَّ
لَكَ لَأَجۡرًا غَيۡرَ مَمۡنُونٖ ٣ وَإِنَّكَ لَعَلَىٰ خُلُقٍ عَظِيمٖ ٤ فَسَتُبۡصِرُ
وَيُبۡصِرُونَ ٥ بِأَييِّكُمُ ٱلۡمَفۡتُونُ ٦ إِنَّ رَبَّكَ هُوَ أَعۡلَمُ بِمَن ضَلَّ
عَن سَبِيلِهِۦ وَهُوَ أَعۡلَمُ بِٱلۡمُهۡتَدِينَ ٧ فَلَا تُطِعِ ٱلۡمُكَذِّبِينَ
٨ وَدُّواْ لَوۡ تُدۡهِنُ فَيُدۡهِنُونَ ٩ وَلَا تُطِعۡ كُلَّ حَلَّافٖ مَّهِينٍ
١٠ هَمَّازٖ مَّشَّآءِۭ بِنَمِيمٖ ١١ مَّنَّاعٖ لِّلۡخَيۡرِ مُعۡتَدٍ أَثِيمٍ ١٢
عُتُلِّۭ بَعۡدَ ذَٰلِكَ زَنِيمٍ ١٣ أَن كَانَ ذَا مَالٖ وَبَنِينَ ١٤ إِذَا تُتۡلَىٰ عَلَيۡهِ
ءَايَٰتُنَا قَالَ أَسَٰطِيرُ ٱلۡأَوَّلِينَ ١٥ سَنَسِمُهُۥ عَلَى ٱلۡخُرۡطُومِ ١٦



**(27) Yayin da alqawari ya cika, suka ga azaba kusa da su, a ranar tashin alqiyama, sai fuskokin kafirai suka canza, suka yi baqi, kuma za a ce musu: "Wannan shi ne abin da kuke nema a duniya, kuna neman a gaggauto shi".**
**(28) Ya kai wannan Manzo ka faxawa waxannan mushirikai masu qaryatawa, kana mai yi musu inkari cewa: "Ku bani labari mana, idan Allah ya karvi rayuwata, waxanda suke tare da ni daga Muminai su ma suka mutu, to wane ne zai tseratar da kafirai daga azaba mai raxaxi?! Babu wanda zai tseratar da su. (29) Ya kai wannan Manzo ka faxawa waxannan mushirikai cewa: "Wanda zai iya tseratar da su daga azaba mai raxaxi shi ne Allah mai rahama, wanda yake kiran ku zuwa bauta masa shi kaxai, don haka mun yi imani da shi, kuma shi kaxai muka dogara da shi a cikin al'amuranmu, to da sannu – ba makawa – zaku san wanda yake cikin vata bayyananne, da wanda yake kan tafarki madaidaici. (30) Ya kai wannan Manzo ka faxawa waxannan mushirikai cewa: "Ku ba ni labari mana, in ruwan da kuke sha ya wayi gari ya shige cikin qasa, ba zaku iya isa gare shi ba, to waye zai zo muku da ruwa mai yawa mai gudana?!. Babu kowa sai Allah.**

# Suratul Qalam

An Saukar Da Ita A Makkah

## Daga Manufofin Surar:

**Bayyana ilimin Annabi (S.A.W) da kyawawan xabi'unsa, domin qarfafa shi, bayan mushirikai sun masa rashin mutunci.**

## Tafsir:

**(1) (Noon) Bayani a kan ire-iren waxannan haruffai ya gabata a farkon Suratul Baqara. Allah ya rantse da alqalami, kuma ya rantse da abin da mutane suke rubutawa da alqalaminsu. (2) Ya kai wannan Manzo, kai ba mahaukaci ba ne dangane da ni'imar da Allah ya yi maka ta Annabta, tabbas kai kuvutacce ne daga hauka, wanda mushirikai suka jefe ka da shi. (3) Haqiqa kana da lada, wanda baya yankewa, a kan wahalar da kake sha wurin isar da saqon Allah, kuma babu wanda zai yi maka gori da wannan lada. (4) Kuma tabbas kai kana kan wasu xabi'u masu girma, waxanda Alqur'ani ya zo da su, lallai kai kana yin aiki da su a bisa mafi kyan tsari.**
**(5) Kuma da sannu zaka gani, haka ma waxannan masu qaryatawar zasu gani. (6) Yayin da gaskiya zata bayyana, za a gane wane ne yake da hauka a tare da shi?!. (7) Haqiqa Ubangijinka -Ya kai wannan Manzo – ya san wane ne ya kauce hanyarsa, kuma ya fi kowa sanin waxanda suka shiriya gare ta, don haka ya san su ne suka vace daga hanyar, kai kuma kai ne wanda ka shiriya zuwa gare ta. (8) Ya kai wannan Manzo kada ka biyewa masu qaryata abin da ka zo da shi. (9) Sun yi burin ina ma a ce ka sassauta musu a kan addini, su ma sai su sassauta maka, kuma su lallava ka. (10) Kada ka biyewa mai yawan rantse-rantse a kan qarya, wulaqantacce.**
**(11) Mai yawan gulmar mutane, mai yawan yawo da annamimanci a tsakanin jama'a, domin ya raba tsakaninsu.**
**(12) Mai yawan hana alheri, mai yi wa mutane ta'addanci a dukiyarsu, da mutuncinsu, da kawunansu, mai yawan laifi da savon Allah. (13) Mai busasshiyar zuciya, mai kaushi, kuma shigege a cikin mutanensa, mai kalen dangi.**
**(14) Kawai don yana da dukiya, da 'ya'ya sai ya yi girman kai ga barin imani da Allah da Manzonsa. (15) Idan ana karanta musa ayoyinmu sai ya ce: "Wannan irin abin da aka rubuta ne daga cikin tatsuniyar mutanen farko".**
**(16) Da sannu zamu sanya alama a kan hancinsa, wadda zata munana halittarsa, kuma ta dauwama a jikinsa.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Manzon Allah (S.A.W) ya siffantu da xabi'un Alqur'ani. 2 - Siffar kafirai siffa ce abar zargi, wadda ya wajaba mumini ya nisance ta, kuma kada ya biyewa masu irinta. 3 - Duk mai yawaita rantsuwa to zai wulaqanta a wurin Allah mai rahama, kuma mutuncinsa ma zai zube a idon mutane.**

إِنَّا بَلَوْنَٰهُمْ كَمَا بَلَوْنَآ أَصْحَٰبَ ٱلْجَنَّةِ إِذْ أَقْسَمُوا۟ لَيَصْرِمُنَّهَا مُصْبِحِينَ ﴿١٧﴾ وَلَا
يَسْتَثْنُونَ ﴿١٨﴾ فَطَافَ عَلَيْهَا طَآئِفٌ مِّن رَّبِّكَ وَهُمْ نَآئِمُونَ ﴿١٩﴾ فَأَصْبَحَتْ
كَٱلصَّرِيمِ ﴿٢٠﴾ فَتَنَادَوْا۟ مُصْبِحِينَ ﴿٢١﴾ أَنِ ٱغْدُوا۟ عَلَىٰ حَرْثِكُمْ إِن كُنتُمْ
صَٰرِمِينَ ﴿٢٢﴾ فَٱنطَلَقُوا۟ وَهُمْ يَتَخَٰفَتُونَ ﴿٢٣﴾ أَن لَّا يَدْخُلَنَّهَا ٱلْيَوْمَ عَلَيْكُم
مِّسْكِينٌ ﴿٢٤﴾ وَغَدَوْا۟ عَلَىٰ حَرْدٍ قَٰدِرِينَ ﴿٢٥﴾ فَلَمَّا رَأَوْهَا قَالُوٓا۟ إِنَّا لَضَآلُّونَ
﴿٢٦﴾ بَلْ نَحْنُ مَحْرُومُونَ ﴿٢٧﴾ قَالَ أَوْسَطُهُمْ أَلَمْ أَقُل لَّكُمْ لَوْلَا تُسَبِّحُونَ
﴿٢٨﴾ قَالُوا۟ سُبْحَٰنَ رَبِّنَآ إِنَّا كُنَّا ظَٰلِمِينَ ﴿٢٩﴾ فَأَقْبَلَ بَعْضُهُمْ عَلَىٰ بَعْضٍ
يَتَلَٰوَمُونَ ﴿٣٠﴾ قَالُوا۟ يَٰوَيْلَنَآ إِنَّا كُنَّا طَٰغِينَ ﴿٣١﴾ عَسَىٰ رَبُّنَآ أَن يُبْدِلَنَا
خَيْرًا مِّنْهَآ إِنَّآ إِلَىٰ رَبِّنَا رَٰغِبُونَ ﴿٣٢﴾ كَذَٰلِكَ ٱلْعَذَابُ ۖ وَلَعَذَابُ ٱلْءَاخِرَةِ
أَكْبَرُ ۚ لَوْ كَانُوا۟ يَعْلَمُونَ ﴿٣٣﴾ إِنَّ لِلْمُتَّقِينَ عِندَ رَبِّهِمْ جَنَّٰتِ ٱلنَّعِيمِ ﴿٣٤﴾
أَفَنَجْعَلُ ٱلْمُسْلِمِينَ كَٱلْمُجْرِمِينَ ﴿٣٥﴾ مَا لَكُمْ كَيْفَ تَحْكُمُونَ ﴿٣٦﴾ أَمْ لَكُمْ
كِتَٰبٌ فِيهِ تَدْرُسُونَ ﴿٣٧﴾ إِنَّ لَكُمْ فِيهِ لَمَا تَخَيَّرُونَ ﴿٣٨﴾ أَمْ لَكُمْ أَيْمَٰنٌ عَلَيْنَا
بَٰلِغَةٌ إِلَىٰ يَوْمِ ٱلْقِيَٰمَةِ ۙ إِنَّ لَكُمْ لَمَا تَحْكُمُونَ ﴿٣٩﴾ سَلْهُمْ أَيُّهُم بِذَٰلِكَ
زَعِيمٌ ﴿٤٠﴾ أَمْ لَهُمْ شُرَكَآءُ فَلْيَأْتُوا۟ بِشُرَكَآئِهِمْ إِن كَانُوا۟ صَٰدِقِينَ ﴿٤١﴾ يَوْمَ
يُكْشَفُ عَن سَاقٍ وَيُدْعَوْنَ إِلَى ٱلسُّجُودِ فَلَا يَسْتَطِيعُونَ ﴿٤٢﴾



**(17) Haqiqa mun jarrabi waxannan mushirikai da fari da yunwa, kamar yadda muka jarrabi masu lambu, lokacin da suka yi rantsuwa cewa zasu girbe amfaninsa da asubahi, cikin gaggawa domin kada mabuqata su ci kayan lambun.**
**(18) Amma basu yi togaciya a cikin rantsuwarsu ba, wato basu ce: "Idan Allah ya yarda ba".**
**(19) Sai Allah ya turowa lambunsu wuta daga sama, ta cinye wannan lambu, a lokacin suna barci, yadda ba zasu iya kare lambun ba.**
**(20) Sai lambun ya koma baqi qirin, kai kace dare ne mai matuqar duhu. (21) Sai sashensu ya kira sashe da asubahi. (22) Suna cewa: ku fito da wuri zuwa ga lambunku, tun kafin talakawa su je, idan har zaku girbe amfanin". (23) Sai suka tafi zuwa ga shukarsu, cikin gaggawa, sashensu yana magana da sashe da murya qasa qasa. (24) Suna cewa juna: "kada ku bar wani talaka mabuqaci ya shigar muku lambu a yau". (25) Suka tafi tun da asubar fari da niyyar su hana kowa ya amfana da 'ya'yan itatuwan. (26) Lokacin da suka ga lambun a qone qurmus, sai sashensu ya cewa sashe: "Haqiqa mun vace hanyar zuwa lambunmu". (27) Kai! Mu fa an haramta mana girbe 'ya'yan itacen nan ne fa, saboda niyyar da muka yi, ta hana miskinai daga gare ta". (28) Sai mafificinnsu ya ce: "Ashe ban faxa muku ba, yayin da kuka yi niyyar yin abin da zaku yi, na hana talakawa amfanin lambunku?! Na ce muku: "Ina ma zaku tsarkake Allah, ku tuba zuwa gare shi. (29) Sai suka ce: "Tsarki ya tabbata ga Ubangijinmu, haqiqa mun kasance waxanda suka zalunci kawunansu, yayin da muka yi niyyar hana talakawa 'ya'yan itacen lambun mu". (30) Sai kuma suka dawo suna yin da na sani, kuma suna yi wa juna magana da take cike da zargin junansu. (31) Sai suka ce a cikin nadama: "Kaiconmu, Haqiqa mun qetare iyaka da hana mabuqata haqqinsu". (32) "Ya kusata Ubangijinmu ya canza mana da mafi alheri daga gonarmu, mu ga Allah kaxai muke kwaxayi, muna fatan afuwa daga gare shi, kuma muna neman alheri daga wajensa". (33) To kamar irin wannan azaba, ta hana su arziki, haka muke azabtar da wanda ya sava mana, kuma tabbas azabar lahira ta fi ta duniya girma, da a ce sun san tsananinta da dauwamarta.**
**(34) Haqiqa masu jin tsoron Allah, ta hanyar kamanta umarninsa, da nisantar abubuwan da ya hana, suna da Aljannatai na ni'ima a wurin Ubangijinsu, suna jin daxi a cikinsu, jin daxin da ba zai yanke ba.**
**(35) Shin yanzu musulmai kamar kafirai a wajen sakamako, kamar yadda mushirikan Makkah suke riyawa?!.**
**(36) Me ya same ku – Ku mushirikai – ta yaya kuke yin irin wannan ja'irin hukuncin karkatacce?!.**
**(37) Ko kuwa kuna da wani littafi da kuke karanto daidaita mai biyayya da mai savo a cikinsa?!.**
**(38) Haqiqa a cikin wannan littafi akwai abin da kuka zava a lahira?. (39) Ko kuwa mun xaukar muku wasu alqawura ne, da muka qarfafa su da rantsuwa, waxanda suka qunshi cewa za a baku abin da kuka zavawa kawunanku a lahira?!. (40) Ya kai wannan Manzo, ka tambayi masu faxar wannan magana kace: shin wane ne zai lamince musu wannan da'awa ta su?!. (41) Ko suna da wasu abokan tarayya ne koma bayan Allah, waxanda suke daidaita su da muminai a wajen sakamako?!. To su zo da abokan tarayyar nasu mana, idan har da gaske suke yi a cikin abin da suke da'awa cewa sun daidaita su da muminai wajen sakamako.**
**(42) Ranar alqiyama tashin hankali zai bayyana a fili, kuma Ubangijinmu zai yaye qwaurinsa, a kirawo mutane zuwa ga yin sujjada, sai Muminai su yi sujjada, sai kafirai da munafikai su rage, su kasa yin sujjadar.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Hana haqqin talaka yana sanya dukiya ta lalace.**
**2 - Gaggauto da uquba a duniya, yana cikin nufin bawa da alheri, don ya tuba ya koma zuwa ga Allah.**
**3 - Mumini da kafiri ba zasu yi daidaita ba a wurin sakamako, kamar yadda siffofinsu basu zama xaya ba.**

خَٰشِعَةً أَبۡصَٰرُهُمۡ تَرۡهَقُهُمۡ ذِلَّةٞۖ وَقَدۡ كَانُواْ يُدۡعَوۡنَ إِلَى ٱلسُّجُودِ وَهُمۡ
سَٰلِمُونَ ٤٣ فَذَرۡنِي وَمَن يُكَذِّبُ بِهَٰذَا ٱلۡحَدِيثِۖ سَنَسۡتَدۡرِجُهُم
مِّنۡ حَيۡثُ لَا يَعۡلَمُونَ ٤٤ وَأُمۡلِي لَهُمۡۚ إِنَّ كَيۡدِي مَتِينٌ ٤٥ أَمۡ تَسۡـَٔلُهُمۡ
أَجۡرٗا فَهُم مِّن مَّغۡرَمٖ مُّثۡقَلُونَ ٤٦ أَمۡ عِندَهُمُ ٱلۡغَيۡبُ فَهُمۡ يَكۡتُبُونَ
٤٧ فَٱصۡبِرۡ لِحُكۡمِ رَبِّكَ وَلَا تَكُن كَصَاحِبِ ٱلۡحُوتِ إِذۡ نَادَىٰ
وَهُوَ مَكۡظُومٞ ٤٨ لَّوۡلَآ أَن تَدَٰرَكَهُۥ نِعۡمَةٞ مِّن رَّبِّهِۦ لَنُبِذَ بِٱلۡعَرَآءِ
وَهُوَ مَذۡمُومٞ ٤٩ فَٱجۡتَبَٰهُ رَبُّهُۥ فَجَعَلَهُۥ مِنَ ٱلصَّٰلِحِينَ
٥٠ وَإِن يَكَادُ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ لَيُزۡلِقُونَكَ بِأَبۡصَٰرِهِمۡ لَمَّا سَمِعُواْ
ٱلذِّكۡرَ وَيَقُولُونَ إِنَّهُۥ لَمَجۡنُونٞ ٥١ وَمَا هُوَ إِلَّا ذِكۡرٞ لِّلۡعَٰلَمِينَ ٥٢

آياتها ٥٢ — سُورَةُ الحَاقَّةِ — ترتيبها ٦٩

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

نصف الحزب ٥٧ ٱلۡحَآقَّةُ ١ مَا ٱلۡحَآقَّةُ ٢ وَمَآ أَدۡرَىٰكَ مَا ٱلۡحَآقَّةُ ٣ كَذَّبَتۡ ثَمُودُ وَعَادُۢ
بِٱلۡقَارِعَةِ ٤ فَأَمَّا ثَمُودُ فَأُهۡلِكُواْ بِٱلطَّاغِيَةِ ٥ وَأَمَّا عَادٞ فَأُهۡلِكُواْ بِرِيحٖ
صَرۡصَرٍ عَاتِيَةٖ ٦ سَخَّرَهَا عَلَيۡهِمۡ سَبۡعَ لَيَالٖ وَثَمَٰنِيَةَ أَيَّامٍ حُسُومٗاۖ فَتَرَى
ٱلۡقَوۡمَ فِيهَا صَرۡعَىٰ كَأَنَّهُمۡ أَعۡجَازُ نَخۡلٍ خَاوِيَةٖ ٧ فَهَلۡ تَرَىٰ لَهُم مِّنۢ بَاقِيَةٖ ٨



**(43) Idanuwansu suna cike da qasqanci, nadama da qasqanci sun lulluve su, alhali a duniya sun kasance ana nemansu da su yi sujjada ga Allah, a lokacin suna cikin lafiyarsu fiye da yadda suke ciki a yau.**
**(44) Ya kai wannan Manzo, ka qyale ni da wanda yake qaryata wannan Alqur'ani, wanda aka saukar maka, da sannu zamu kora su zuwa ga azaba, mataki bayan mataki, ta inda basu san cewa wannan makirci ne da talala ba.**
**(45) Zan bar su wani xan lokaci domin su ci gaba da aikata laifi, Haqiqa talala ta da kaidi na ga ma'abota kafirci da qaryatawa suna da qarfi, ba zasu kubce mini ba, kuma ba zasu kuvuta daga uquba ta ba.**
**(46) Ya kai wannan Manzo, shin kana neman wani lada ne daga wurinsu a kan kiransu da kake yi, don haka suke ganin ka xora musu nauyi mai girma, sai suka bijire maka?!. A haqiqanin gaskiya ba haka lamarin yake ba, kai baka neman wani lada a wurinsu, to me ya hana su, su bi ka?!.**
**(47) Ko kuwa suna da ilimin gaibu ne, da suke rubuta abin da suke so na hujjoji daga gare shi, waxanda suke jayayya da kai da su?!.**
**(48) Ya kai wannan Manzo, ka yi haquri da abin da Ubangijinka ya hukunta na jinkirta musu, kada ka kasance kamar ma'abocin kifi Annabi Yunus (A.S) wurin damuwa a kan abin da mutanensa suke kai, lokacin da ya kira Ubangijinsa yana cikin damuwa a cikin duhun teku, da duhun cikin kifi.**
**(49) Ba don rahamar Allah ta riske shi ba, da wannan kifi ya wurgo shi a wurin da babu komai, yana abin zargi. (50) Sai Ubangijinsa ya zave shi, ya sanya shi daga cikin bayinsa nagari.**
**(51) Waxanda suka kafirce wa Allah, kuma suka qaryata Manzonsa sun kusa su sumar da kai da idanuwansu, saboda tsananin kallon da suke yi maka, yayin da suka ji wannan Alqur'ani, wanda aka saukar maka da shi, suna cewa – saboda bin zuciyarsu, da bijirewa gaskiya -: "Manzon da ya zo da wannan Alqur'anin tabbas mahaukaci ne". (52) Alqur'anin da aka saukar maka ba komai ba ne face wa'azi da tunatarwa ga mutane da aljanu.**

# Suratul Haqqah

An Saukar Da Ita A Makkah

**Daga Manufofin Surar:** **Tabbatuwar faruwar tashin alqiyama, domin gasgata bayanan Alqur'ani, da kuma alqawarin farin ciki ga Muminai, da alqawarin asara ga masu qaryatawa.**

**Tafsir:** **(1) Allah yana ambaton lokacin tashin alqiyama, wanda zai tabbata a kan kowa da kowa.**
**(2) Sannan yana girmama lamarinta da tambayar cewa: "Mece ce mai faruwa?". (3) Me ya sanar da kai mece ce mai faruwa? (4) Samudawa mutanen Annabi Salihu sun qaryata, da Adawa mutanen Annabi Hudu, duk sun qaryata da ranar tashin alqiyama, wadda take firgita mutane, saboda tsananin abubuwan tsoron da suke cikinta.**
**(5) Amma Samudawa haqiqa Allah ya halakar da su da tsawa, wadda ta kai matuqa wajen tsanani da ban tsoro.**
**(6) Amma Adawa haqiqa Allah ya halakar da su, ta hanyar iska mai tsananin sanyi, wadda ya kai matuqa wurin qeqashewa a kansu. (7) Allah ya aiko musu da ita har tsawon darare bakwai, da wuni takwas, tana qarar da su gaba xaya, sai ka ga mutane a cikin gidajensu an halaka su, suna zube a qasa, kai ka ce bishiyoyin dabino ne, da suka farfaxi a qasa. (8) Shin kana kana ganin wata rai da ta yi saura a cikinsu, bayan azabar da ta sauka a kansu?!.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:** 1 - **Haquri xabi'a ce mai kyau, kuma ya wajaba masu kira ga Allah su siffantu da shi.** 2 - **Tuba yana kankare laifukan da suka rigaye shi, kuma yana sa Allah ya zavi mutum, ya sanya shi daga cikin bayi nagari.** 3 - **Kala – kalar azabar da Allah yake aikawa kafirai da masu savo, tana nuna cikar ikon Allah da cikar adalcinsa.**

وَجَآءَ فِرۡعَوۡنُ وَمَن قَبۡلَهُۥ وَٱلۡمُؤۡتَفِكَٰتُ بِٱلۡخَاطِئَةِ ٩ فَعَصَوۡاْ رَسُولَ
رَبِّهِمۡ فَأَخَذَهُمۡ أَخۡذَةٗ رَّابِيَةً ١٠ إِنَّا لَمَّا طَغَا ٱلۡمَآءُ حَمَلۡنَٰكُمۡ فِي ٱلۡجَارِيَةِ
١١ لِنَجۡعَلَهَا لَكُمۡ تَذۡكِرَةٗ وَتَعِيَهَآ أُذُنٞ وَٰعِيَةٞ ١٢ فَإِذَا نُفِخَ فِي ٱلصُّورِ
نَفۡخَةٞ وَٰحِدَةٞ ١٣ وَحُمِلَتِ ٱلۡأَرۡضُ وَٱلۡجِبَالُ فَدُكَّتَا دَكَّةٗ وَٰحِدَةٗ ١٤
فَيَوۡمَئِذٖ وَقَعَتِ ٱلۡوَاقِعَةُ ١٥ وَٱنشَقَّتِ ٱلسَّمَآءُ فَهِيَ يَوۡمَئِذٖ وَاهِيَةٞ
١٦ وَٱلۡمَلَكُ عَلَىٰٓ أَرۡجَآئِهَاۚ وَيَحۡمِلُ عَرۡشَ رَبِّكَ فَوۡقَهُمۡ يَوۡمَئِذٖ ثَمَٰنِيَةٞ
١٧ يَوۡمَئِذٖ تُعۡرَضُونَ لَا تَخۡفَىٰ مِنكُمۡ خَافِيَةٞ ١٨ فَأَمَّا مَنۡ أُوتِيَ كِتَٰبَهُۥ
بِيَمِينِهِۦ فَيَقُولُ هَآؤُمُ ٱقۡرَءُواْ كِتَٰبِيَهۡ ١٩ إِنِّي ظَنَنتُ أَنِّي مُلَٰقٍ حِسَابِيَهۡ
٢٠ فَهُوَ فِي عِيشَةٖ رَّاضِيَةٖ ٢١ فِي جَنَّةٍ عَالِيَةٖ ٢٢ قُطُوفُهَا دَانِيَةٞ ٢٣
كُلُواْ وَٱشۡرَبُواْ هَنِيٓـَٔۢا بِمَآ أَسۡلَفۡتُمۡ فِي ٱلۡأَيَّامِ ٱلۡخَالِيَةِ ٢٤ وَأَمَّا مَنۡ أُوتِيَ
كِتَٰبَهُۥ بِشِمَالِهِۦ فَيَقُولُ يَٰلَيۡتَنِي لَمۡ أُوتَ كِتَٰبِيَهۡ ٢٥ وَلَمۡ أَدۡرِ مَا حِسَابِيَهۡ
٢٦ يَٰلَيۡتَهَا كَانَتِ ٱلۡقَاضِيَةَ ٢٧ مَآ أَغۡنَىٰ عَنِّي مَالِيَهۡۜ ٢٨ هَلَكَ عَنِّي سُلۡطَٰنِيَهۡ
٢٩ خُذُوهُ فَغُلُّوهُ ٣٠ ثُمَّ ٱلۡجَحِيمَ صَلُّوهُ ٣١ ثُمَّ فِي سِلۡسِلَةٖ ذَرۡعُهَا
سَبۡعُونَ ذِرَاعٗا فَٱسۡلُكُوهُ ٣٢ إِنَّهُۥ كَانَ لَا يُؤۡمِنُ بِٱللَّهِ ٱلۡعَظِيمِ ٣٣
وَلَا يَحُضُّ عَلَىٰ طَعَامِ ٱلۡمِسۡكِينِ ٣٤ فَلَيۡسَ لَهُ ٱلۡيَوۡمَ هَٰهُنَا حَمِيمٞ ٣٥



**(9) Fir'auna da waxanda suka gabace shi daga cikin Al'ummu sun zo, haka ma alqaryun da aka azabtar da su ta hanyar juya samansu ya koma qasansu, su ne mutanen Annabi Luxu, da waxanda aka halakar saboda ayyukan zunubi da shirka. (10) Kowannensu sai ya savawa Manzonsa, wanda aka aiko masa, suka qaryata shi, sai Allah ya kama su, qari a kan abin da zai halakar da su. (11) Haqiqa mu a lokacin da ruwa ya qetare iyaka wurin yin sama, sai muka xauki waxanda kuke cikin tsatson su a cikin jirgin ruwa mai gudu, wanda Annabi Nuhu (A.S) ya yi da umarninmu, sai wannan ya zama xaukan ku ne. (12) Mun yi haka ne domin mu sanya wannan jirgin ruwa da labarinsa su zama wa'azi, da za a riqa kafa hujja da shi a kan halakar da kafirai, da tseratar da masu imani, kuma kunne mai kiyayewa ya kiyaye. (13) Idan Mala'ikan da aka wakilta ya yi busa a qaho ya yi busa guda xaya, ita ce busa ta biyu. (14) Kuma aka xage qasa da duwatsu, aka dandaqe su dandaqewa guda xaya mai tsanani, qasa da duwatsunta suka yi laushi. (15) A ranar da hakan zata faru, a ranar alqiyama zata afku. (16) Sama zata kekkece a wannan rana domin saukowar Mala'iku daga cikinta, sama a wannan rana mai rauni ce, bayan ta kasance mai qarfi mai haxe da juna. (17) Kuma Mala'iku zasu kasance a gefenta da vangarorinta, kuma a wannan rana mai girma Mala'iku makusanta guda takwas masu girma ne suke xauke da al'arshin Ubangijinka. (18) A wannan rana za a bijiro da ku – Ya ku mutane - ga Allah, babu wani da zai vuya ga Allah daga cikinku, ko mene ne, face Allah ya san da shi, kuna yana ganinsa. (19) Amma wanda aka bawa littafin ayyukansa a hannun damansa, zaka ji yana faxa cikin farin ciki da annashuwa yana cewa: "Ku karvi littafin ayyukana ku karanta". (20) "Haqiqa ni na riga na sani, na kuma tabbatar a duniya cewa za a tashe ni bayan na mutu, kuma tabbas zan haxu da sakamako na". (21) Don haka shi yana cikin rayuwa yardaddiya, saboda abin da ya gani na ni'ima dauwamammiya. (22) Yana cikin Aljanna maxaukakiya mai daraja.**
**(23) 'Ya'yan itatuwanta suna kusa da mai tsinkarsu. (24) Kuma za a ce musu cikin girmamawa a gare su: "Ku ci ku sha, ba tare da kun cutu ba, saboda abin da kuka gabatar na ayyuka masu kyau a kwanakin da suka wuce a duniya". (25) Amma duk wanda aka ba shi littafin ayyukansa a hannun hagunsa, to wannan zai faxa cikin tsananin nadama ya ce: "Kaicona, ina ma ba a ba ni littafina ba, saboda munanan ayyukan da suke cikinsa, waxanda zasu sa a azabtar da ni". (26) Kaicona ga shi ban san yaya hisabi na zai kasance ba**
**(27) Kaicona dama a ce mutuwar da na yi, ta kasance ba a tashi bayanta har abada.**
**(28) Dukiyata bata kare ni daga azabar Allah ba da komai.**
**(29) Kuma hujjata ta vace min, haka ma duk wani abin da na dogara da shi na qarfi da matsayi.**
**(30) Sai a ce: "Ku kama shi - Ya ku Mala'iku - ku haxa hannayensa da wuyansa".**
**(31) Sannan ku saka shi a cikin wuta, domin ya xanxani zafinta.**
**(32) Sannan ku xaure shi da sarka, wadda tsawonta yake kamu saba'in.**
**(33) Tabbas shi ya kasance baya yin imani da Allah mai girma.**
**(34) Kuma baya kwaxaitar da waninsa ya ciyar da miskinai.**
**(35) To a yau ranar alqiyama ba shi da wani makusanci da zai kare shi daga azaba.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa: 1 - Baiwar da Allah ya yi wa mahaifi, baiwa ce ga xa, kuma tana wajabta godiya ga Allah. 2 - Ciyar da mabuqaci, da kwaxaitarwa a kan hakan, yana daga cikin abubuwan da suke kariya ne daga azabar wuta. 3 - Tsananin azaba ranar alqiyama, yana wajabta neman kariya daga wannan tsanani, ta hanyar imani da aiki nagari.**

وَلَا طَعَامٌ إِلَّا مِنْ غِسْلِينٍ ٣٦ لَّا يَأْكُلُهُۥٓ إِلَّا ٱلْخَٰطِـُٔونَ ٣٧ فَلَآ أُقْسِمُ
بِمَا تُبْصِرُونَ ٣٨ وَمَا لَا تُبْصِرُونَ ٣٩ إِنَّهُۥ لَقَوْلُ رَسُولٍ كَرِيمٍ ٤٠ وَمَا هُوَ
بِقَوْلِ شَاعِرٍ قَلِيلًا مَّا تُؤْمِنُونَ ٤١ وَلَا بِقَوْلِ كَاهِنٍ قَلِيلًا مَّا تَذَكَّرُونَ
تَنزِيلٌ مِّن رَّبِّ ٱلْعَٰلَمِينَ ٤٢ وَلَوْ تَقَوَّلَ عَلَيْنَا بَعْضَ ٱلْأَقَاوِيلِ ٤٣ ٤٤
لَأَخَذْنَا مِنْهُ بِٱلْيَمِينِ ٤٥ ثُمَّ لَقَطَعْنَا مِنْهُ ٱلْوَتِينَ ٤٦ فَمَا مِنكُم
مِّنْ أَحَدٍ عَنْهُ حَٰجِزِينَ ٤٧ وَإِنَّهُۥ لَتَذْكِرَةٌ لِّلْمُتَّقِينَ ٤٨ وَإِنَّا
لَنَعْلَمُ أَنَّ مِنكُم مُّكَذِّبِينَ ٤٩ وَإِنَّهُۥ لَحَسْرَةٌ عَلَى ٱلْكَٰفِرِينَ
وَإِنَّهُۥ لَحَقُّ ٱلْيَقِينِ ٥٠ فَسَبِّحْ بِٱسْمِ رَبِّكَ ٱلْعَظِيمِ ٥١ ٥٢

سُورَةُ المَعَارِجِ — آيَاتُهَا ٤٤ — تَرْتِيبُهَا ٧٠

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

سَأَلَ سَآئِلٌۢ بِعَذَابٍ وَاقِعٍ ١ لِّلْكَٰفِرِينَ لَيْسَ لَهُۥ دَافِعٌ ٢
مِّنَ ٱللَّهِ ذِى ٱلْمَعَارِجِ ٣ تَعْرُجُ ٱلْمَلَٰٓئِكَةُ وَٱلرُّوحُ إِلَيْهِ
فِى يَوْمٍ كَانَ مِقْدَارُهُۥ خَمْسِينَ أَلْفَ سَنَةٍ ٤ فَٱصْبِرْ صَبْرًا جَمِيلًا
إِنَّهُمْ يَرَوْنَهُۥ بَعِيدًا ٥ وَنَرَىٰهُ قَرِيبًا ٦ يَوْمَ تَكُونُ ٱلسَّمَآءُ ٧
كَٱلْمُهْلِ ٨ وَتَكُونُ ٱلْجِبَالُ كَٱلْعِهْنِ ٩ وَلَا يَسْـَٔلُ حَمِيمٌ حَمِيمًا ١٠



36 Kuma ba shi da wani abinci da ake ciyar da shi sai daga ruwan qurjin 'yan wuta.
37 Babu mai cin wannan abincin sai masu zunubai da savon Allah.
38 Allah ya rantse da abin da kuke gani.
39 Kuma ya rantse da abin da bakwa iya gani.
40 Tabbas Alqur'ani maganar Allah ne, Manzonsa mai girma yake karantar da mutane shi. 41 Ba maganar mawaqi ba ce, domin baya kama da salon waqa, sai dai kaxan ne kuke yin imani.
42 Kuma ba maganar matsafi ba ne, domin maganganun matsafa sun sha bamban da wannan Alqur'ani, sai dai kaxan ne kuke tunawa.
43 Sai dai shi abin saukarwa ne daga Ubangijin halitta gaba xaya.
44 Da a ce Muhammad ya qirqiri wasu maganganu da bamu faxa ba.
45 Da mun damqe shi, mun kama shi da qarfinmu, da ikonmu.
46 Sannan da mun tsinke masa jijiyar da take haxe da zuciya.
47 Kuma babu wani daga cikinku da zai kare shi daga gare mu daga cikinku, don haka zai yi wuya ya faxi abin da bamu faxa ba, saboda ku.
48 Haqiqa Alqur'ani wa'azi ne ga masu tsoron Ubangijinsu ta hanyar kamanta umarninsa, da nisantar abubuwan da ya hana.
49 Kuma haqiqa mun san daga cikinku akwai waxanda suke qaryata wannan Alqur'ani.
50 Kuma tabbas qaryata Alqur'ani nadama ce mai girma ranar alqiyama.
51 Kuma tabbas Alqur'ani gaskiya ne tsantsa, wadda babu kokwanto ko shakka a cikinsa cewa daga wurin Allah yake. 52 Ya kai wannan Manzo, ka tsarkake Ubangijinka daga duk abin da bai dace da shi ba, kuma ka ambaci sunan Ubangijinka mai girma.

# Suratul Ma'arij

An Saukar Da Ita A Makkah

**Daga Manufofin Surar:** Qarfafa saukar da azaba a kan kafirai, da kuma samun ni'ima ga masu gasgatawa a ranar sakamako.

**Tafsir:** 1 Wani mai addu'a daga cikin mushirikai ya yi wa kansa da mutanensa addu'ar azaba, idan har da gaske azabar mai afkuwa ce. Ya yi wannan ne don izgili, amma tabbas azabar zata afku a ranar tashin alqiyama.
2 Ga masu kafirce wa Allah, wannan azaba bata da makawa. 3 Daga Allah ma'abocin xaukaka da darajoji da falaloli da ni'imomi. 4 Mala'iku suna hawa zuwa gare shi, da Mala'ika jibrilu a cikinsu, a ranar alqiyama, wanda wani yini ne mai tsawo, gwargwadonsa shi ne shekara dubu hamsin na kwanakin duniya. 5 Ya kai wannan Manzo ka yi haquri, haqurin da babu raki ko kai qara a cikinsa. 6 Su suna ganin wannan azabar da ake ta yin maganarta, kamar ba zata yi wu ba. 7 Mu kuma muna ganin ta a kusa take, kuma zata faru babu makawa.
8 Ranar da sama zata kasance kamar narkakkiyar azurfa ko zinare, ko makamantansu.
9 Duwatsu kuma su zama kamar auduga, wajen a rashin nauyi.
10 Makusanci ba zai tambayi makusancinsa halin da yake ciki ba, saboda kowa a cikinsu ya shagalta da kansa.

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

1 - Tsarkake Alqur'ani daga kasancewa waqa ko bokanci. 2 - Haxarin yi wa Allah mai tsarki qarya.
3 - Kyakkyawan haquri shi ne wanda mai shi yake neman lada da shi a wurin Allah, kuma baya kai qara ga wanin Allah.

يبصرونهم يود المجرم لو يفتدي من عذاب يومئذ ببنيه ١١
وصاحبته وأخيه ١٢ وفصيلته التي تؤويه ١٣ ومن في الأرض جميعا
ثم ينجيه ١٤ كلا إنها لظى ١٥ نزاعة للشوى ١٦ تدعو من أدبر
وتولى ١٧ وجمع فأوعى ١٨ إن الإنسان خلق هلوعا ١٩ إذا مسه الشر ثلاثة أرباع الحزب ٥٧
جزوعا ٢٠ وإذا مسه الخير منوعا ٢١ إلا المصلين ٢٢ الذين هم
على صلاتهم دائمون ٢٣ والذين في أموالهم حق معلوم ٢٤ للسائل
والمحروم ٢٥ والذين يصدقون بيوم الدين ٢٦ والذين هم من عذاب
ربهم مشفقون ٢٧ إن عذاب ربهم غير مأمون ٢٨ والذين هم
لفروجهم حافظون ٢٩ إلا على أزواجهم أو ما ملكت أيمانهم
فإنهم غير ملومين ٣٠ فمن ابتغى وراء ذلك فأولئك هم العادون ٣١
والذين هم لأماناتهم وعهدهم راعون ٣٢ والذين هم بشهاداتهم قائمون
٣٣ والذين هم على صلاتهم يحافظون ٣٤ أولئك في جنات مكرمون ٣٥
فمال الذين كفروا قبلك مهطعين ٣٦ عن اليمين وعن الشمال
عزين ٣٧ أيطمع كل امرئ منهم أن يدخل جنة نعيم ٣٨ كلا إنا خلقناهم
مما يعلمون ٣٩ فلا أقسم برب المشارق والمغارب إنا لقادرون ٤٠



**(11) Kowane mutum zai ga makusancinsa, ba zai vuya a gare shi ba, amma duk da haka ba wanda zai tambayi wani, saboda tashin hankalin wannan rana, wanda ya cancanci shiga wuta zai yi burin ina ma zai gabatar da 'yayansa zuwa ga azaba a maimakonsa. (12) Kuma ya fanshi kansa da matarsa da xan'uwansa. (13) Ko kuma ya fanshi kansa da danginsa na kusa, waxanda suke tsayawa tare da shi a lokacin tsanani. (14) Ko kuma ya fanshi kansa da waxanda suke bayan qasa gaba xaya, daga mutune da aljanu da sauransu, don wannan fansar ya kuvutar da shi daga azabar wuta. (15) Sai dai al'amrin ba kamar yadda wannan mai laifi yake buri ba ne, saboda wutar lahira ce, wanda take ci da ruruwa. (16) Tana raba fatar kai da inda take saboda tsananin zafinta da ruruwarta. (17) Tana kiran wanda ya bijirewa gaskiya, ya yi nesa da ita, bai yi imani da ita ba, ballantana ya yi aiki da ita. (18) Kuma ya tara dukiya, ya yi rowar ciyar da ita a kan tafarkin Allah. (19) Haqiqa an halicci mutum da tsananin kwaxayi.**
**(20) Idan cuta ta same shi, ta rashin lafiya ko talauci, sai ya zama mai qarancin haquri.**
**(21) Idan kuma abin farin ciki ya same shi, kamar wadata, sai ka gan shi mai yawan rowa da qin ciyarwa a tafarkin Allah. (22) Amma ban da masu yin sallah, su, sun kuvuta daga waxannan munanan siffofi. (23) Su ne waxanda suke dauwama a kan sallolinsu, basa shagalta ga barinsu, kuma suna yin su a kan lokutansu da aka qayyade. (24) Kuma su ne waxanda a cikin dukiyoyinsu akwai wani rabo da aka iyakance shi, aka wajabta shi. (25) Suna bada wannan rabo ga wanda ya tambaye su, da kuma wanda bai tambaye su ba, daga cikin waxanda ba su da abin hannunsu. (26) Kuma su ne waxanda suke gasgatawa da ranar tashin alqiyama, ranar da Allah zai sakawa kowa da abin da ya cancance shi. (27) Kuma su ne waxanda suke tsoron azabar Ubangijinsu, duk da abin da suka gabatar na ayyuka nagari. (28) Tabbas azabar Ubangijinsu abar tsoro ce, mai hankali baya amincewa da ita. (29) Kuma su ne waxanda suke kiyaye al'aurarsu, ta hanyar suturce ta, da nisanta ta ga da alfasha. (30) Sai dai ga matayensu, ko kuma abin da suka mallaka na bayi, to su ba ababen zargi ba ne, don sun jiyar da kansu daxi da su, ta hanyar kwanciya ko da abin da bai kai hakan ba. (31) Kuma duk wanda ya nemi jin daxi, ba da abin da aka ambata na matan aure da bayi ba, to waxannan su ne masu qetare iyakokin Allah.**
**(32) Kuma su ne waxanda suke kiyaye sirrin da aka basu, na dukiya ko waninta, da alqawuran da suka yi wa mutane, basa yin ha'inci, kuma basa warware alqawarinsu. (33) Su ne waxanda suke tsayawa a kan bada shaida kamar yadda ake so, kusanci ko qiyayya basa musu tasiri. (34) Su ne waxanda suke kiyaye sallolinsu, ta hanyar yin su a kan lokutansu, cikin tsarki da nutsuwa, babu abin da yake xauke musu hanlaki daga barin sallah.**
**(35) Waxanda aka siffanta da waxancan siffofin da aka ambata suna cikin Aljannatai, suna ababen girmama, da abin da za su samu na ni'ima daumammiya, da ganin fuskar Allah mai girma. (36) Ya kai wannan Manzo me ya ja waxannan mushirikai daga cikin mutanenka suke gaggawar qaryata ka?!. (37) Kuma suna keweye da kai ta dama da hagu, jama'a jama'a. (38) Shin kowanne daga cikinsu ya tsammanin Allah ya shigar da shi Aljanna mai ni'ima, ya samu ni'imar da take cikinta dauwamammiya, alhali yana nan a kan kafircinsa?!. (39) To gaskiya lamarin ba kamar yadda suke tunani ba ne, haqiqa mun halicce su daga abin da suka sani, mun halicce su daga wani ruwa wukaqantacce, don haka su raunana ne basa mallakar amfani ko cuta ga kansu, to ta yaya zasu yi girman kai?!.**
**(40) Allah yayi rantsuwa da Ubangijin mahudar rana da wata, a kan tabbas mu masu iko ne.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa: 1 - Tsananin azabar wuta, ta yadda 'yan wuta za su yi burin su kuvuta daga cikinta ta kowace hanya da suka sani a duniya. 2 - Sallah tana cikin manya manyan abubuwa masu kankare laifuka a duniya, kuma ake samun kariya da ita daga faxawa wutar lahira.**
**3 - Tsoron azabar Allah yana janyo mutum ya yawaita aikin alheri.**

(41) Akan mu canza su da waninsu waxanda suke tsoron Allah, su kuma mu halakar da su, baza mu gaza yin haka ba, kuma mu ba waxanda za a rinjaya ba ne a duk lokacin da muka yi nufin halakar da su da canza su da waninsu. (42) Ya kai wannan Manzo, ka qyale su su kutsa cikin abin da suke kai na vata da varna, kuma su yi wasa a rayuwarsu ta duniya, har lokacin da zasu haxu da ranar alqiyama, wadda aka yi musu alqawarinta a cikin Alqur'ani. (43) Ranar da zasu fita daga cikin qaburburansu, suna masu gaggawa, kai ka ce rigegeniya suke yi zuwa ga wata alama da aka saka a tsakaninsu. (44) Idanuwansu suna cike da qasqanci, qasqanci kuma ya lulluve su. Wannan ita ce ranar da ake yi musu alqawarinta a duniya, amma suka kasance basa damuwa da ita.

# Suratu Nuhu

An Saukar Da Ita A Makkah

## Daga Manufofin Surar:

**Haqurin masu kira zuwa ga Allah, da jihadinsu wurin da'awa, ta hanyar qissar Annabi Nuhu (A.S), don qarfafa Muminai, da tsoratar da masu qaryatawa.**



عَلَىٰٓ أَن نُّبَدِّلَ خَيْرًا مِّنْهُمْ وَمَا نَحْنُ بِمَسْبُوقِينَ ﴿٤١﴾ فَذَرْهُمْ
يَخُوضُوا۟ وَيَلْعَبُوا۟ حَتَّىٰ يُلَٰقُوا۟ يَوْمَهُمُ ٱلَّذِى يُوعَدُونَ ﴿٤٢﴾ يَوْمَ
يَخْرُجُونَ مِنَ ٱلْأَجْدَاثِ سِرَاعًا كَأَنَّهُمْ إِلَىٰ نُصُبٍ يُوفِضُونَ ﴿٤٣﴾
خَٰشِعَةً أَبْصَٰرُهُمْ تَرْهَقُهُمْ ذِلَّةٌ ذَٰلِكَ ٱلْيَوْمُ ٱلَّذِى كَانُوا۟ يُوعَدُونَ ﴿٤٤﴾

ترتيبها ٧١ — سُورَةُ نُوح — آياتها ٢٨

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

إِنَّآ أَرْسَلْنَا نُوحًا إِلَىٰ قَوْمِهِۦٓ أَنْ أَنذِرْ قَوْمَكَ مِن قَبْلِ أَن يَأْتِيَهُمْ
عَذَابٌ أَلِيمٌ ﴿١﴾ قَالَ يَٰقَوْمِ إِنِّى لَكُمْ نَذِيرٌ مُّبِينٌ ﴿٢﴾ أَنِ ٱعْبُدُوا۟
ٱللَّهَ وَٱتَّقُوهُ وَأَطِيعُونِ ﴿٣﴾ يَغْفِرْ لَكُم مِّن ذُنُوبِكُمْ وَيُؤَخِّرْكُمْ
إِلَىٰٓ أَجَلٍ مُّسَمًّى ۚ إِنَّ أَجَلَ ٱللَّهِ إِذَا جَآءَ لَا يُؤَخَّرُ ۖ لَوْ كُنتُمْ تَعْلَمُونَ ﴿٤﴾
قَالَ رَبِّ إِنِّى دَعَوْتُ قَوْمِى لَيْلًا وَنَهَارًا ﴿٥﴾ فَلَمْ يَزِدْهُمْ دُعَآءِىٓ إِلَّا
فِرَارًا ﴿٦﴾ وَإِنِّى كُلَّمَا دَعَوْتُهُمْ لِتَغْفِرَ لَهُمْ جَعَلُوٓا۟ أَصَٰبِعَهُمْ فِىٓ
ءَاذَانِهِمْ وَٱسْتَغْشَوْا۟ ثِيَابَهُمْ وَأَصَرُّوا۟ وَٱسْتَكْبَرُوا۟ ٱسْتِكْبَارًا
﴿٧﴾ ثُمَّ إِنِّى دَعَوْتُهُمْ جِهَارًا ﴿٨﴾ ثُمَّ إِنِّىٓ أَعْلَنتُ لَهُمْ وَأَسْرَرْتُ
لَهُمْ إِسْرَارًا ﴿٩﴾ فَقُلْتُ ٱسْتَغْفِرُوا۟ رَبَّكُمْ إِنَّهُۥ كَانَ غَفَّارًا ﴿١٠﴾



## Tafsir:

(1) Haqiqa mun aiko Annabi Nuhu zuwa ga mutanensa, yana kiran su, don ya tsoratar da su azaba mai raxaxi, saboda abin da suke kai na shirka da Allah. (2) Sai Annabi Nuhu ya cewa mutanensa: "Ya ku mutanena, ni mai gargaxi ne a bayyane gare ku, game da wata azaba da take jiran ku idan har baku tuba zuwa ga Allah ba".

(3) Abin da gargaxina ya qunsa shi ne, in ce da ku: "Ku bautawa Allah shi kaxai, kada ku haxa shi da kowa a wurin bauta, kuma ku ji tsoronsa ta hanyar kamanta umarninsa, da nisantar haninsa, kuma ku yi min biyayya a cikin umarnin da nake yi muku".

(4) Tabbas idan kuka aikata haka, Allah zai gafarta muku zunubanku waxanda basu da alaqa da haqqin bayi, kuma ya tsawaita lokacinku a rayuwa, zuwa wani lokaci iyakantacce a wurin Allah, sai ku raya qasa matuqar kun tsaya a kan hakan. Haqiqa mutuwa idan ta zo ba a jinkirtawa, da kun san haka, da kun yi gaggawa zuwa ga imani da Allah da tuba daga abin da kuke kai na shirka da vata".

(5) Annabi Nuhu ya ce: "Ya Ubangiji Haqiqa na kira mutanena zuwa ga bautarka  da kaxaita ka, dare da rana, babu fashi".

(6) Amma kira na bai qara musu komai ba sai gujewa da nisa daga abin da nake kiransu zuwa gare shi.

(7) Kuma duk lokacin na kirawo su zuwa ga abin da zai sa a gafarta musu zunubansu, na bauta maka kai kaxai, da yi maka xa'a, da yi wa Manzonka xa'a, sai su toshe kunnuwansu da 'yan yatsunsu, domin su hana kansu jin abin da nake faxa, kuma su rufe fuskokinsu da tufafinsu, don kada su ganni, kuma sun ci gaba da abin da suke yi na shirka, sannan sun yi girman kai daga karvar abin da nake kiransu zuwa gare shi, da miqa wuya gare shi.

(8) Sannan ya Ubangiji na kirawo su a bayyane.

(9) Sannan na xaga sautina gare su domin na isar musu da saqonka, kuma na kirawo su a voye, kuma na kirawo su da sauti qasa qasa, na yi amfani da salo kala-kala.

(10) Na ce da su: "Ya ku mutanena, ku nemi gafarar Allah, ta hanyar tuba gare shi, Haqiqa shi mai tsarki mai yawan gafara ne ga zunuban duk wanda ya tuba gare shi daga cikin bayinsa".

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

1 - Haxarin rafkana ga barin lahira.
2 - Bautar Allah da tsoronsa, suna haifar da gafarar zunubai.
3 - Ci gaba da kira ga Allah, da kuma yin salo kala-kala wajibi ne a kan masu kira zuwa ga Allah.

يُرۡسِلِ ٱلسَّمَآءَ عَلَيۡكُم مِّدۡرَارٗا ١١ وَيُمۡدِدۡكُم بِأَمۡوَٰلٖ وَبَنِينَ وَيَجۡعَل
لَّكُمۡ جَنَّٰتٖ وَيَجۡعَل لَّكُمۡ أَنۡهَٰرٗا ١٢ مَّا لَكُمۡ لَا تَرۡجُونَ لِلَّهِ وَقَارٗا ١٣
وَقَدۡ خَلَقَكُمۡ أَطۡوَارًا ١٤ أَلَمۡ تَرَوۡاْ كَيۡفَ خَلَقَ ٱللَّهُ سَبۡعَ سَمَٰوَٰتٖ
طِبَاقٗا ١٥ وَجَعَلَ ٱلۡقَمَرَ فِيهِنَّ نُورٗا وَجَعَلَ ٱلشَّمۡسَ سِرَاجٗا ١٦
وَٱللَّهُ أَنۢبَتَكُم مِّنَ ٱلۡأَرۡضِ نَبَاتٗا ١٧ ثُمَّ يُعِيدُكُمۡ فِيهَا وَيُخۡرِجُكُمۡ
إِخۡرَاجٗا ١٨ وَٱللَّهُ جَعَلَ لَكُمُ ٱلۡأَرۡضَ بِسَاطٗا ١٩ لِّتَسۡلُكُواْ مِنۡهَا
سُبُلٗا فِجَاجٗا ٢٠ قَالَ نُوحٞ رَّبِّ إِنَّهُمۡ عَصَوۡنِي وَٱتَّبَعُواْ مَن لَّمۡ يَزِدۡهُ
مَالُهُۥ وَوَلَدُهُۥٓ إِلَّا خَسَارٗا ٢١ وَمَكَرُواْ مَكۡرٗا كُبَّارٗا ٢٢ وَقَالُواْ
لَا تَذَرُنَّ ءَالِهَتَكُمۡ وَلَا تَذَرُنَّ وَدّٗا وَلَا سُوَاعٗا وَلَا يَغُوثَ وَيَعُوقَ
وَنَسۡرٗا ٢٣ وَقَدۡ أَضَلُّواْ كَثِيرٗاۖ وَلَا تَزِدِ ٱلظَّٰلِمِينَ إِلَّا ضَلَٰلٗا ٢٤
مِّمَّا خَطِيٓـَٰٔتِهِمۡ أُغۡرِقُواْ فَأُدۡخِلُواْ نَارٗا فَلَمۡ يَجِدُواْ لَهُم مِّن دُونِ
ٱللَّهِ أَنصَارٗا ٢٥ وَقَالَ نُوحٞ رَّبِّ لَا تَذَرۡ عَلَى ٱلۡأَرۡضِ مِنَ ٱلۡكَٰفِرِينَ
دَيَّارًا ٢٦ إِنَّكَ إِن تَذَرۡهُمۡ يُضِلُّواْ عِبَادَكَ وَلَا يَلِدُوٓاْ إِلَّا فَاجِرٗا
كَفَّارٗا ٢٧ رَّبِّ ٱغۡفِرۡ لِي وَلِوَٰلِدَيَّ وَلِمَن دَخَلَ بَيۡتِيَ مُؤۡمِنٗا
وَلِلۡمُؤۡمِنِينَ وَٱلۡمُؤۡمِنَٰتِۖ وَلَا تَزِدِ ٱلظَّٰلِمِينَ إِلَّا تَبَارَۢا ٢٨



**(11) Tabbas idan kuka aikata hakan, Allah zai saukar muku da ruwan sama, a kai a kai, duk lokacin da kuka buqaci hakan, fari ba zai same ku ba.**

**(12) Kuma ya baku dukiya da ‘ya’ya masu yawa, kuma ya sanya muku gonaki da zaku riqa ci daga ‘ya’yan itacensu, kuma ya sanya muku qoramu da zaku riqa shan ruwansu, kuna shayar da shukarku da dabbobinku.**

**(13) “To me ya same ku ne - Ya ku mutanena - ba kwa tsoron girman Allah, kuke sava masa, babu abin da ya dame ku?!”.**

**(14) Alhali ya halicce ku mataki bayan mataki, daga xigon maniyyi, sannan gudan jini, sannan kuma gudan tsoka.**

**(15) Shin baku ga yadda Allah ya halicci sammai guda bakwai ba, wata saman a kan wata?!.**

**(16) Kuma ya sanya wata a saman duniya, domin ya haska wa mutanen da suke bayan qasa, kuma ya sanya rana ita ma ta zama mai haske.**

**(17) Allah ne ya halicce ku daga qasa, ta hanyar halittar babanku Annabi Adamu daga turvaya, sannan kuma kuna samun abin da zaku ci daga abin da turvayar take fitarwa.**

**(18) Sannan ya sake komar da ku cikin qasar bayan mutuwarku, sannan ya sake fitar da ku domin tashin alqiyama, fitarwa ta haqiqa.**

**(19) Allah ne ya sanya muku qasa ta zama a shimfixa, kuma a shirye don zama a kanta.**

**(20) Kuma da fatan zaku bi hanyoyi masu faxi da yalwa a cikinta don neman halal.**

**(21) Annabi Nuhu ya ce: “Ya Ubangiji, Haqiqa mutanena sun sava min, cikin abin da na umarce su da shi na kaxaitaka, da bauta maka, qananansu sun bi shugabanninsu waxanda ka yi wa ni’imar ‘ya’ya da dukiya, abin da ka yi musu na ni’ima bai qara musu komai ba sai vata”.**

**(22) Kuma manya daga cikinsu suka ci gaba da yin makirci, makirci mai girma, ta hanyar tunzura qanannansu su yi wauta ga Annabi Nuhu.**

**(23) Suka cewa mabiyansu: “Kada ku bar bautar allolinku, kada ku bar bautar gumakanku, su ne, Wadda da Suwa’a, da Yagusa, da Ya’uqa, da Nasra”.**

**(24) Haqiqa sun vatar da mutane masu yawa da waxannan gumakan nasu. Ya Ubangiji kada ka qarawa waxanda suka zalunci kansu, ta hanyar zarcewa a kan kafirci da savo komai, sai vacewa daga hanyar gaskiya.**

**(25) Sakamakon laifukan da suka aikata, aka nutsar da su a cikin ruwan Xufana a duniya, kuma aka shigar da su wuta bayan mutuwarsu kai tsaye, basu samu wasu mataimaka ba koma bayan Allah, da zasu tseratar da su daga nutsewa da azabar wuta.**

**(26) Sai Annabi Nuhu ya ce, yayin da Allah ya ba shi labarin cewa, babu wanda zai yi imani da shi daga cikin mutanensa, sai wanda ya riga ya yi, don haka sai ya ce: “Ya Ubangiji kada ka bar wani mai kai-kawo ko yin motsi daga cikin kafirai a bayan qasa”.**

**(27) Tabbas ya Ubangijinmu idan ka bar su, ka jinkirta musu zasu vatar da bayinka Muminai, kuma baza su haifa ba sai fajiri wanda ba zai yi maka xa’a ba, da mai tsaurin kafirci, wanda ba zai godewa ni’imarka ba.**

**(28) Ya Ubangiji ka gafarta min zunubaina, kuma ka gafartawa iyayena, kuma ka gafartawa duk wanda ya shiga gidana yana mai imani, kuma ka gafartawa muminai maza da mata, kuma kada ka qarawa waxanda suka zalunci kansu da kafirci da savo komai sai halaka da asara”.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:** **1 - Neman gafarar Allah sababi ne na saukar ruwan sama, da samun ‘ya’ya da dukiya mai yawa. 2 - Rawar da manya suke takawa wajen vatar da qanana abu ne da yake a fili. 3 - Zunubai sabubba ne na halaka a duniya, da azaba a lahira.**

# Suratul Jinni

An Saukar Da Ita A Makkah

## Daga Manufofin Surar:

**Gasgata saukar da Alqur'ani, da kuma cewa shi daga Allah yake, ta hanyar yadda aljanu suka yi imani da shi, da bayanin vacin abin da mushirikai suke rayawa dangane da aljanu.**

سُورَةُ الجِنِّ — آياتها ٢٨ — ترتيبها ٧٢

الحزب ٥٨

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

قُلْ أُوحِيَ إِلَيَّ أَنَّهُ اسْتَمَعَ نَفَرٌ مِّنَ الْجِنِّ فَقَالُوا إِنَّا سَمِعْنَا قُرْآنًا
عَجَبًا ١ يَهْدِي إِلَى الرُّشْدِ فَآمَنَّا بِهِ وَلَن نُّشْرِكَ بِرَبِّنَا أَحَدًا ٢
وَأَنَّهُ تَعَالَىٰ جَدُّ رَبِّنَا مَا اتَّخَذَ صَاحِبَةً وَلَا وَلَدًا ٣ وَأَنَّهُ كَانَ
يَقُولُ سَفِيهُنَا عَلَى اللَّهِ شَطَطًا ٤ وَأَنَّا ظَنَنَّا أَن لَّن تَقُولَ الْإِنسُ
وَالْجِنُّ عَلَى اللَّهِ كَذِبًا ٥ وَأَنَّهُ كَانَ رِجَالٌ مِّنَ الْإِنسِ يَعُوذُونَ بِرِجَالٍ
مِّنَ الْجِنِّ فَزَادُوهُمْ رَهَقًا ٦ وَأَنَّهُمْ ظَنُّوا كَمَا ظَنَنتُمْ أَن لَّن يَبْعَثَ
اللَّهُ أَحَدًا ٧ وَأَنَّا لَمَسْنَا السَّمَاءَ فَوَجَدْنَاهَا مُلِئَتْ حَرَسًا
شَدِيدًا وَشُهُبًا ٨ وَأَنَّا كُنَّا نَقْعُدُ مِنْهَا مَقَاعِدَ لِلسَّمْعِ فَمَن
يَسْتَمِعِ الْآنَ يَجِدْ لَهُ شِهَابًا رَّصَدًا ٩ وَأَنَّا لَا نَدْرِي أَشَرٌّ أُرِيدَ
بِمَن فِي الْأَرْضِ أَمْ أَرَادَ بِهِمْ رَبُّهُمْ رَشَدًا ١٠ وَأَنَّا مِنَّا الصَّالِحُونَ
وَمِنَّا دُونَ ذَٰلِكَ كُنَّا طَرَائِقَ قِدَدًا ١١ وَأَنَّا ظَنَنَّا أَن لَّن نُّعْجِزَ
اللَّهَ فِي الْأَرْضِ وَلَن نُّعْجِزَهُ هَرَبًا ١٢ وَأَنَّا لَمَّا سَمِعْنَا الْهُدَىٰ
آمَنَّا بِهِ فَمَن يُؤْمِن بِرَبِّهِ فَلَا يَخَافُ بَخْسًا وَلَا رَهَقًا ١٣



## Tafsir:

**(1) Ya kai wannan Manzo, ka cewa Al'ummarka: "Allah ya yi min wahayi cewa wasu jama'a daga cikin aljanu sun saurari karatuna na Alqur'ani a inda ake kira da (Baxnu Nakhla) yayin da aljanun suka koma ga mutanensu sai suka ce da su: "Tabbas mun ji wata magana da ake karanta ta mai ban-mamaki da fasahar bayani da azanci". (2) "Wannan maganan da muka ji tana xauke da aqida da magana da aiki daidaitattu, don haka sai muka yi imani da ita, kuma ba zamu haxa kowa da Ubangijinmu wanda ya saukar da wannan magana ba, a wajen bauta masa".**

**(3) Kuma mun yi imani lallai shi Ubangijinmu ya girmama, bai riqi mata ko wani xa ba, kamar yadda mushirikai suke faxa.**

**(4) Kuma tabbas Iblis ya kasance yana faxar magana marar kyau a kan Allah, kamar danganta masa mata ko xa. Tsarki ya tabbata a gare shi.**

**(5) Kuma mu mun yi zaton mushirikai daga cikin mutane da aljanu ba qarya suke yi wa Allah ba, a yayin da suke cewa Allah yana da mata da xa, don haka sai muka gasgata maganarsu, muna koyi da su.**

**(6) Kuma lallai a lokacin jahiliyya akwai wasu mazaje daga cikin mutane da suke neman tsari a wurin wasu mazaje daga cikin aljanu, a yayin da suka sauka a wani wuri mai ban-tsoro, sai ka ji xayansu yana cewa: "Ina neman tsari da jagoran wannan kwari daga sharrin wawayen mutanensa". Wannan ya sa wasu mazaje da cikin mutane suka qara jin tsoron wasu mazaje da aljannu.**

**(7) Kuma mutane sun yi zato kamar yadda ku – Aljanu - kuka yi zaton cewa Allah ba zai tashi kowa bayan ya mutu ba, don ya yi masa hisabi da sakayya". (8) Kuma mu mun nemi jin labarin sama, sai muka samu saman an cika ta da tsaro mai tsanani na Mala'iku, suna gadinta daga satar jin da muke aikatawa, kuma an cika ta da wuta mai ruruwa, wadda ake jifan duk wanda ya kusanci sama da ita.**

**(9) Kuma mu a da mun samu wasu wurare a sama da muke sauraren abin da Mala'iku suke tattaunawa, sai mu ba wa bokayen da suke qasa labari, amma yanzu lamarin ya canza, duk wanda yanzu a cikinmu ya yi satar ji, to zai haxu da tauraro mai xauke da wuta mai ci, wadda aka tanadar masa, da ya kusanto sai a jefa masa wannan tauraron ya qone shi.**

**(10) Kuma mu ba mu san dalilin wannan tsaro mai tsanani ba, shin sharri ake nufi ga mutanen da suke bayan qasa, ko kuwa Allah yana nufin su da wani alheri ne?!. Haqiqa dai labaran sama sun yanke mana.**

**(11) Kuma mu taron aljanu, a cikin mu akwai masu tsoron Allah, mutanen kirki, kuma a cikin mu akwai kafirai fasiqai, Haqiqa mun kasance kala-kala, masu ra'ayi daban daban. (12) Kuma mun sakankance cewa bamu isa mu gujewa Allah ba, idan ya nufe mu da wani lamari, kuma bamu isa mu guje masa ba, saboda yana kewaye da mu.**

**(13) Kuma a lokacin da muka ji Alqur'ani mai shiryarwa ga hanya mafi kyau, sai muka yi imani da shi, kuma duk wanda ya yi imani da Ubangijinsa, to kada ya ji tsoron a tauye masa ladan ayyukansa ba, ko kuma a qara masa wasu zunuban qari a kan zunubansa da ya aikata.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:** **1 - Alqur'ani yana da tasiri matuqa ga wanda yake jin sa da zuciya mai kyau. 2 - Neman taimako daga aljanu shirka ne, kuma ana yi wa mai aikata shi uquba da ba shi savanin abin da yake nema a duniya. 3 - Vacewar bokanci da aiko Annabi (S.A.W).**

**4 - Yana daga cikar ladabin mumini kada ya danganta sharri ga Allah.**

وَأَنَّا مِنَّا ٱلۡمُسۡلِمُونَ وَمِنَّا ٱلۡقَٰسِطُونَۖ فَمَنۡ أَسۡلَمَ فَأُوْلَٰٓئِكَ
تَحَرَّوۡاْ رَشَدٗا ١٤ وَأَمَّا ٱلۡقَٰسِطُونَ فَكَانُواْ لِجَهَنَّمَ حَطَبٗا ١٥
وَأَلَّوِ ٱسۡتَقَٰمُواْ عَلَى ٱلطَّرِيقَةِ لَأَسۡقَيۡنَٰهُم مَّآءً غَدَقٗا ١٦ لِّنَفۡتِنَهُمۡ
فِيهِۚ وَمَن يُعۡرِضۡ عَن ذِكۡرِ رَبِّهِۦ يَسۡلُكۡهُ عَذَابٗا صَعَدٗا ١٧ وَأَنَّ
ٱلۡمَسَٰجِدَ لِلَّهِ فَلَا تَدۡعُواْ مَعَ ٱللَّهِ أَحَدٗا ١٨ وَأَنَّهُۥ لَمَّا قَامَ عَبۡدُ ٱللَّهِ
يَدۡعُوهُ كَادُواْ يَكُونُونَ عَلَيۡهِ لِبَدٗا ١٩ قُلۡ إِنَّمَآ أَدۡعُواْ رَبِّي وَلَآ أُشۡرِكُ
بِهِۦٓ أَحَدٗا ٢٠ قُلۡ إِنِّي لَآ أَمۡلِكُ لَكُمۡ ضَرّٗا وَلَا رَشَدٗا ٢١ قُلۡ إِنِّي
لَن يُجِيرَنِي مِنَ ٱللَّهِ أَحَدٞ وَلَنۡ أَجِدَ مِن دُونِهِۦ مُلۡتَحَدًا ٢٢ إِلَّا بَلَٰغٗا
مِّنَ ٱللَّهِ وَرِسَٰلَٰتِهِۦۚ وَمَن يَعۡصِ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ فَإِنَّ لَهُۥ نَارَ جَهَنَّمَ
خَٰلِدِينَ فِيهَآ أَبَدًا ٢٣ حَتَّىٰٓ إِذَا رَأَوۡاْ مَا يُوعَدُونَ فَسَيَعۡلَمُونَ
مَنۡ أَضۡعَفُ نَاصِرٗا وَأَقَلُّ عَدَدٗا ٢٤ قُلۡ إِنۡ أَدۡرِيٓ أَقَرِيبٞ مَّا تُوعَدُونَ
أَمۡ يَجۡعَلُ لَهُۥ رَبِّيٓ أَمَدًا ٢٥ عَٰلِمُ ٱلۡغَيۡبِ فَلَا يُظۡهِرُ عَلَىٰ غَيۡبِهِۦٓ
أَحَدًا ٢٦ إِلَّا مَنِ ٱرۡتَضَىٰ مِن رَّسُولٖ فَإِنَّهُۥ يَسۡلُكُ مِنۢ بَيۡنِ
يَدَيۡهِ وَمِنۡ خَلۡفِهِۦ رَصَدٗا ٢٧ لِّيَعۡلَمَ أَن قَدۡ أَبۡلَغُواْ رِسَٰلَٰتِ
رَبِّهِمۡ وَأَحَاطَ بِمَا لَدَيۡهِمۡ وَأَحۡصَىٰ كُلَّ شَيۡءٍ عَدَدَۢا ٢٨



**(14) Kuma mu daga cikin mu akwai musilmai, masu biyayya ga Allah da yi masa xa'a, kuma akwai waxanda suka karkace daga hanyar gaskiya da daidaito. Duk wanda ya ranqwafa ga Allah ta hanyar yi masa xa'a, da aiki nagari, to lallai waxannan su ne suka nufi shiriya da aikata daidai. (15) Amma waxanda suka karkacewa hanyar shiriya, to waxannan za su kasance makamashi ga wutar jahannama, ana ruruta ta da su da makamantansu daga cikin mutane.**
**(16) Kamar yadda aka yi masa wahayi cewa wasu jama'a daga ciki aljanu sun saurari wahayin da aka yi masa na Alqur'ani, to haka ma aka yi masa wahayi cewa da mutane da aljanu zasu tsaya akan tafarkin Musulunci, kuma suka yi aiki da abin da yake cikinsa, da Allah ya shayar da su ruwa mai yawa, kuma ya kwararo musu ni'imomi masu yawa. (17) Domin mu jarraba su, shin zasu gode ni'imar da Allah ya yi musu, ko kuwa zasu butulce mata? Duk wanda ya bijirewa Alqur'ani, da abin da yake cikinsa na wa'azi, Ubangijinsa zai shigar da shi cikin azaba mai wahala, wadda ba zai iya jure mata ba. (18) Lallai dukkan masallatai na Allah ne, ba na waninsa ba, don haka kada ku kira wani tare da Allah a cikinsu, sai ku zama kamar Yahudawa da Nasara a cikin cocinansu da gidajen bautarsu. (19) Kuma shi lokacin da bawan Allah, Muhammad (S.A.W) ya tashi yana bautar Ubangijinsu a Vaxnu Nakhla, sai aljanu suka kusa su yi masa cincirindo saboda cinkoso, yayin da suke jin karatunsa na Alqur'ani.**
**(20) Ya kai wanna Manzo, ka cewa waxannan mushirikai: "Kaxai ina kiran Ubangijina shi kaxai, kuma ba zan tava haxa shi da wani ba a wurin bauta, ko wane ne". (21) Ka ce da su: "Haqiqa ni bana mallakar kare ku daga wata cuta wadda Allah ya qaddara muku, kuma bana mallakara jawo muku wani amfani da Allah ya hana ku shi".**
**(22) Ka ce da su: "Babu wanda zai tseratar da ni a wurin Allah idan na sava masa, kuma ba zan samu wata mafaka da zan fake daga gare shi ba". (23) Abin da nake mallaka kawai shi ne na isar muku da abin da Allah ya umarce ni in isar da shi zuwa gare ku, da saqon da ya aiko ni da shi zuwa gare ku. Duk wanda ya savawa Allah da Manzonsa, to makomarsa ita ce shiga wutar Jahannama, yana mai dauwama a cikinta, ba zai fita ba har abada".**
**(24) Kafirai ba zasu gushe akan kafircinsu ba, har zuwa lokacin da zasu ga abin da aka yi musu alqawari a duniya na azaba, a wannan lokacin zasu san waye yake da mataimaki mai rauni, kuma a ranar za su san waye yake da mataimaka kaxan. (25) Ya ka wannan Manzo, ka faxa waxannan mushirikai masu inkarin tashin alqiyama, ka ce da su: "Ban sani ba, shin anan kusa ne azabar da ake alqawarta muku zata same ku, ko kuwa tana da wani lokaci daban wanda babu wanda ya san shi sai Allah". (26) Allah mai tsarki shi ne masanin duk wani gaibu, babu abin da yake vuya a gare shi, kuma baya tsikayar da wani a kan gaibunsa, yana wanzuwa mai kevantuwa da sanin sa.**
**(27) Sai dai ga wanda Allah ya yarda da shi na daga Manzo, to yana iya tsinkayar da shi abin da ya ga dama, kuma yana aiko da masu gadi daga cikin Mala'iku suna gadin wannan gaibun, don kada wani wanda ba Manzo ba ya tsinkayi wannan gaibun.**
**(28) Sannan kuma don wannan Manzo ya san cewa Manzannin da suka gabace shi sun isar da saqonnin da Ubangijinsu ya umarce su da isarwa, saboda kulawar da Allah ya ba shi, kuma Allah ya kewaye abin da yake wurin Mala'ikunsa da Manzanninsa da iliminsa, don haka babu abin da yake vuya a gare shi daga cikinsu, ya kuma qididdige adadin komai, babu abin da yake vuya a gare shi.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Zalunci sababi ne na shiga wuta. 2 - Muhimmancin tsayawa akan tafarki madaidaici, a wajen tabbatar da kyakkyawar manufa. 3 - An kare wahayi daga shaixanu su yi wasa da shi.**

# Suratul Muzzamil

An Saukar Da Ita A Makkah

آياتها ٢٠ سُورَةُ المُزَّمِّلِ ترتيبها ٧٣

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

يَٰٓأَيُّهَا ٱلْمُزَّمِّلُ ١ قُمِ ٱلَّيْلَ إِلَّا قَلِيلًا ٢ نِّصْفَهُۥٓ أَوِ ٱنقُصْ مِنْهُ قَلِيلًا
٣ أَوْ زِدْ عَلَيْهِ وَرَتِّلِ ٱلْقُرْءَانَ تَرْتِيلًا ٤ إِنَّا سَنُلْقِى عَلَيْكَ قَوْلًا
ثَقِيلًا ٥ إِنَّ نَاشِئَةَ ٱلَّيْلِ هِىَ أَشَدُّ وَطْـًٔا وَأَقْوَمُ قِيلًا ٦ إِنَّ لَكَ فِى
ٱلنَّهَارِ سَبْحًا طَوِيلًا ٧ وَٱذْكُرِ ٱسْمَ رَبِّكَ وَتَبَتَّلْ إِلَيْهِ تَبْتِيلًا ٨
رَّبُّ ٱلْمَشْرِقِ وَٱلْمَغْرِبِ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ فَٱتَّخِذْهُ وَكِيلًا ٩ وَٱصْبِرْ
عَلَىٰ مَا يَقُولُونَ وَٱهْجُرْهُمْ هَجْرًا جَمِيلًا ١٠ وَذَرْنِى وَٱلْمُكَذِّبِينَ
أُو۟لِى ٱلنَّعْمَةِ وَمَهِّلْهُمْ قَلِيلًا ١١ إِنَّ لَدَيْنَآ أَنكَالًا وَجَحِيمًا ١٢
وَطَعَامًا ذَا غُصَّةٍ وَعَذَابًا أَلِيمًا ١٣ يَوْمَ تَرْجُفُ ٱلْأَرْضُ وَٱلْجِبَالُ
وَكَانَتِ ٱلْجِبَالُ كَثِيبًا مَّهِيلًا ١٤ إِنَّآ أَرْسَلْنَآ إِلَيْكُمْ رَسُولًا شَٰهِدًا
عَلَيْكُمْ كَمَآ أَرْسَلْنَآ إِلَىٰ فِرْعَوْنَ رَسُولًا ١٥ فَعَصَىٰ فِرْعَوْنُ ٱلرَّسُولَ
فَأَخَذْنَٰهُ أَخْذًا وَبِيلًا ١٦ فَكَيْفَ تَتَّقُونَ إِن كَفَرْتُمْ يَوْمًا
يَجْعَلُ ٱلْوِلْدَٰنَ شِيبًا ١٧ ٱلسَّمَآءُ مُنفَطِرٌۢ بِهِۦ كَانَ وَعْدُهُۥ مَفْعُولًا
١٨ إِنَّ هَٰذِهِۦ تَذْكِرَةٌ فَمَن شَآءَ ٱتَّخَذَ إِلَىٰ رَبِّهِۦ سَبِيلًا ١٩



**Daga Manufofin Surar:** **Ambaton guzuri na ruhi wanda masu kira zuwa ga Allah ya kamata su samu, wajen tunkarar wahalhalu da masifun duniya, da kuma qarfafa Annabi (S.A.W) da tsoratar da waxanda suke qaryata shi.**

**Tafsir:** **(1) Ya kai wanda ya lulluva da tufafinsa (Ana nufin Annabi S.A.W). (2) Ka yi sallah a cikin dare, ban da kaxan daga cikinsa. (3) Idan ka ga dama ka sallaci rabinsa, ko kuma ka sallaci qasa da rabinsa kaxan, har zuwa xaya bisa uku. (4) Ko kuma ka qara a kan rabinsa, har ka kai biyu bisa uku, kuma ka bayyana Alqur'ani idan kana karanta shi, ka bi a sannu sannu cikin karatunsa. (5) Tabbas haqiqa mu, zamu xora maka – Ya kai wannan Manzo - nauyin Alqur'ani, saboda shi magana ce mai nauyi, domin abin da yake cikinsa na farillai, da haddi, da hukunce-hukunce, da ladubba, da sauransu. (6) Tabbas lokutan dare su ne suka fi dacewa da zuciya wajen karatun Alqur'ani, kuma suka fi zama daidai wajen magana. (7) Kuma haqiqa kana da hidimomin da kake yi a cikin yini, waxanda suke shagaltar da kai daga barin karatun Alqur'ani, don haka ka yi sallah a cikin dare. (8) Kuma ka ambaci Allah ka tuna shi da zikiri kala-kala, kuma ka yanke komai ka koma zuwa gare shi, ta hanyar tsarkake zuciya da bauta masa shi kaxai. (9) Ubangijin mahudar rana da mafaxarta, babu abin bauta wa da gaskiya sai shi, don haka ka riqe shi ya zamar maka abin dogaro, wanda zaka dogara a gare shi a cikin dukkan lamuranka gaba xaya. (10) Kuma ka yi haquri da maganganun masu qaryatawa, kamar izgilancinsu, da zagi. kuma ka qaurace musu qauracewar da babu cutarwa a cikinta. (11) Kada ka damu da lamarin masu qaryatawa, ma'abota jin daxi da rayuwar duniya, ka qyale ni da su kawai, ka jira su kaxan, har ajalinsu ya zo. (12) Haqiqa a wurin mu a lahira, muna da maruruwa da sasari masu nauyi, da wuta kuma mai ci ganga -ganga.**

**(13) Da abinci wanda yake shaqe wuya, saboda tsananin xacinsa, da azaba mai raxaxi, qari akan abin da ya gabata.**

**(14) Wannan azaba zata samu masu qaryatawa ne, ranar da qasa da duwatsu zasu girgiza, a ranar duwatsu zasu zama kamar yashin da ya watse saboda tsananin tsoro. (15) Haqiqa mun aiko muku da Manzo, domin ya zama mai shaida akan ayyukanku a ranar tashin alqiyama, kamar yadda muka aika manzo ga Fir'auna, wato Annabi Musa (A.S). (16) Amma sai Fir'auna ya qaryata Manzon da aka aika masa daga Ubangijinsa, sai muka yi masa uquba mai tsanani a duniya ta hanyar nutsar da shi a teku, a lahira kuma da azabar wuta, don haka kada ku savawa Manzonku, sai abin da ya same shi ya same ku. (17) Ta yaya zaku kare kanku, ku kiyaye kanku, daga wata rana mai tsanani da tsawo, ranar da kawunan yara suke furfura, saboda tsananin tsoro da tsawon wannan rana, idan har kuka kafirce da Allah, kuma kuka qaryata Manzonsa. (18) Sama kanta mai tsagewa ce saboda tsoron wannan rana. kuma alqawarin Allah tabbatacce ne babu makawa.**

**(19) Haqiqa wannan wa'azin da ya qunshi abubuwan da zasu faru a ranar tashin alqiyama na tashin hankali da tsanani, tunatarwa ne da Muminai suke amfana da shi, don haka duk wanda ya ga dama sai ya riqi hanyar da zata sadar da shi ga Ubangijinsu.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:** **1 - Muhimmancin tsayuwar dare, da karatun Alqur'ani, da ambaton Allah, da haquri ga mai kira zuwa ga Allah. 2 - Nutsuwar da zukata ke samu a cikin dare yana da tasiri wurin samun hadda da kuma kyakkyawar fahimta. 3 - Mutum ba zai iya xaukar nauye nauye ba har sai ya samu tarbiyya gamsasshiya da zata taimaka masa ya yi hakan. 4 - Jin daxi da yalwatawa cikinsa yana hana mutum bin hanyar Allah.**

الحِزْب ٥٨

۞ إِنَّ رَبَّكَ يَعْلَمُ أَنَّكَ تَقُومُ أَدْنَىٰ مِن ثُلُثَيِ ٱلَّيْلِ وَنِصْفَهُۥ وَثُلُثَهُۥ وَطَآئِفَةٌ
مِّنَ ٱلَّذِينَ مَعَكَ ۚ وَٱللَّهُ يُقَدِّرُ ٱلَّيْلَ وَٱلنَّهَارَ ۚ عَلِمَ أَن لَّن تُحْصُوهُ فَتَابَ
عَلَيْكُمْ ۖ فَٱقْرَءُوا۟ مَا تَيَسَّرَ مِنَ ٱلْقُرْءَانِ ۚ عَلِمَ أَن سَيَكُونُ مِنكُم مَّرْضَىٰ
وَءَاخَرُونَ يَضْرِبُونَ فِى ٱلْأَرْضِ يَبْتَغُونَ مِن فَضْلِ ٱللَّهِ ۙ وَءَاخَرُونَ
يُقَـٰتِلُونَ فِى سَبِيلِ ٱللَّهِ ۖ فَٱقْرَءُوا۟ مَا تَيَسَّرَ مِنْهُ ۚ وَأَقِيمُوا۟ ٱلصَّلَوٰةَ وَءَاتُوا۟
ٱلزَّكَوٰةَ وَأَقْرِضُوا۟ ٱللَّهَ قَرْضًا حَسَنًا ۚ وَمَا تُقَدِّمُوا۟ لِأَنفُسِكُم مِّنْ خَيْرٍ تَجِدُوهُ
عِندَ ٱللَّهِ هُوَ خَيْرًا وَأَعْظَمَ أَجْرًا ۚ وَٱسْتَغْفِرُوا۟ ٱللَّهَ ۖ إِنَّ ٱللَّهَ غَفُورٌ رَّحِيمٌۢ ٢٠

آياتها ٥٦ — سُورَةُ المُدَّثِّر — ترتيبها ٧٤

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَـٰنِ ٱلرَّحِيمِ

يَـٰٓأَيُّهَا ٱلْمُدَّثِّرُ ١ قُمْ فَأَنذِرْ ٢ وَرَبَّكَ فَكَبِّرْ ٣ وَثِيَابَكَ فَطَهِّرْ ٤
وَٱلرُّجْزَ فَٱهْجُرْ ٥ وَلَا تَمْنُن تَسْتَكْثِرُ ٦ وَلِرَبِّكَ فَٱصْبِرْ ٧ فَإِذَا نُقِرَ
فِى ٱلنَّاقُورِ ٨ فَذَٰلِكَ يَوْمَئِذٍ يَوْمٌ عَسِيرٌ ٩ عَلَى ٱلْكَـٰفِرِينَ غَيْرُ يَسِيرٍ ١٠
ذَرْنِى وَمَنْ خَلَقْتُ وَحِيدًا ١١ وَجَعَلْتُ لَهُۥ مَالًا مَّمْدُودًا ١٢ وَبَنِينَ
شُهُودًا ١٣ وَمَهَّدتُّ لَهُۥ تَمْهِيدًا ١٤ ثُمَّ يَطْمَعُ أَنْ أَزِيدَ ١٥ كَلَّآ ۖ إِنَّهُۥ
كَانَ لِـَٔايَـٰتِنَا عَنِيدًا ١٦ سَأُرْهِقُهُۥ صَعُودًا ١٧ إِنَّهُۥ فَكَّرَ وَقَدَّرَ ١٨



(20) **Haqiqa Ubangijinka – Ya kai wannan Manzo - ya san cewa wani lokaci kana sallatar qasa da biyun bisa ukun dare, wani lokacin kuma kana sallatar rabin dare, ko xaya bisa ukunsa a wani lokacin, haka nan wasu jama'a daga cikin muminai suna tsayuwa tare da kai. Allah ne yake qaddara dare da yini, yake qididdige sa'o'insu, don haka Allah ya sani ba zaku iya kiyaye sa'a'o'in dare da rana gaba xaya ba, don haka idan aka ce ku sallaci mafi yawancin sa'o'in dare hakan zai yi muku wahala, don haka Allah ya karvi tubanku, yanzu ku sallaci abin da ya sauwaqa daga cikin dare. Kuma Allah ya san a cikinku – Ya ku muminai – za a samu marasa lafiya, waxanda rashin lafiya ta galavaitar da su, wasu kuma suna tafiye –tafiye don neman arziki, wasu kuma suna yaqar kafirai don neman yardar Allah, kuma don kalmar Allah ta zama a sama da komai, to duk waxannan tsayuwar dare zata yi musu wahala, don haka ku sallaci abin da ya sauwaqa a gare ku daga cikin dare, ku yi sallar farilla a siffa mafi cika da kyau, ku bada zakkar dukiyoyinku, sannan ku ciyar da dukiyoyinku saboda Allah, duk abin da kuka gabatar ga kawunanku na alheri zaku same shi mafi alheri da girman lada a wurin Allah, ku nemi gafara daga wajen Allah, Haqiqa Allah mai yawan gafara ne ga wanda ya tuba daga cikin bayinsa, kuma mai jinqan su ne.**

# Suratul Muddassir

An Saukar Da Ita A Makkah

## Daga Manufofin Surar:

**Umarni da yin kira zuwa ga Allah, da kuma bayanin mummunan narko ga masu qaryatawa da kiran.**

## Tafsir:

**(1) Ya kai wanda ya lulluve da tufafinsa (Shi ne Annabi S.A.W)**
**(2) Ka tashi ka tsoratar da mutane azabar Allah. (3) Kuma ka girmama Ubangijinka.**
**(4) Kuma ka tsarkake kanka daga zunubai, da tufafinka daga najasa.**
**(5) Kuma ka nisanci bautar gumaka. (6) Kuma kada ka yi wa Ubangijinka gori wai don ka yawaita ayyuka nagari.**
**(7) Kuma ka yi haquri don Allah a kan abin da kake haxuwa da shi na cutarwa. (8) Idan aka yi busa a cikin qaho, busa ta biyu. (9) To wannan rana, rana ce mai tsanani.**
**(10) Ga waxanda suka kafirce wa Allah da Manzanninsa ba mai sauqi ba ce. (11) Ya kai wanna Manzo ka qyale ni da wanda na halicce shi, shi kaxai a cikin mahaifiyarsa, ba tare da dukiya ba ko 'ya'ya ba, (Shi ne Walid bin Mugirah)**
**(12) Kuma na bashi dukiya mai yawa. (13) Na ba shi 'ya'ya, waxandan suke tare da shi, suna zuwa wuraren taro tare da shi, basa rabuwa da shi don tafiya wani wuri, saboda yawan dukiyarsa.**
**(14) Na yalwata masa a cikin rayuwa, da arziki, da 'ya'ya, dukkan yalwatawa.**
**(15) Sannan tare da kafirce min da ya yi, yana kwaxayin in qara masa, bayan duk wannan abin da na ba shi.**
**(16) To lamarin ba kamar yadda yake tunani ba ne, tabbas shi ya kasance mai taurin kai da qaryata ayoyinmu, waxanda muka saukarwa Manzonmu.**
**(17) Da sannu zan xora masa azaba mai wahala, wadda ba zai iya xauka ba.**
**(18) Haqiqa wannan kafirin, wanda na yi masa ni'ima da waxancan ni'imomi, ya tsaya ya yi tunani game da abin da zai faxa a kan Alqur'ani, don ya vata shi, kuma ya qaddara hakan a cikin zuciyarsa.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxanda Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Wahala tana jawo sassauci a shari'a. 2 - Wajabcin yin tsarki daga dukkan qazanta a fili da voye.**
**3 - Ni'imar Allah ga fajiri talala ce mai kamar sake, ba girmamawa ba ce a gare shi.**

فَقُتِلَ كَيْفَ قَدَّرَ ﴿١٩﴾ ثُمَّ قُتِلَ كَيْفَ قَدَّرَ ﴿٢٠﴾ ثُمَّ نَظَرَ ﴿٢١﴾ ثُمَّ عَبَسَ وَبَسَرَ
﴿٢٢﴾ ثُمَّ أَدْبَرَ وَٱسْتَكْبَرَ ﴿٢٣﴾ فَقَالَ إِنْ هَٰذَآ إِلَّا سِحْرٌ يُؤْثَرُ ﴿٢٤﴾ إِنْ هَٰذَآ
إِلَّا قَوْلُ ٱلْبَشَرِ ﴿٢٥﴾ سَأُصْلِيهِ سَقَرَ ﴿٢٦﴾ وَمَآ أَدْرَىٰكَ مَا سَقَرُ ﴿٢٧﴾
لَا تُبْقِي وَلَا تَذَرُ ﴿٢٨﴾ لَوَّاحَةٌ لِّلْبَشَرِ ﴿٢٩﴾ عَلَيْهَا تِسْعَةَ عَشَرَ ﴿٣٠﴾ وَمَا جَعَلْنَآ
أَصْحَٰبَ ٱلنَّارِ إِلَّا مَلَٰٓئِكَةً ۙ وَمَا جَعَلْنَا عِدَّتَهُمْ إِلَّا فِتْنَةً لِّلَّذِينَ كَفَرُوا۟
لِيَسْتَيْقِنَ ٱلَّذِينَ أُوتُوا۟ ٱلْكِتَٰبَ وَيَزْدَادَ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓا۟ إِيمَٰنًا ۙ وَلَا يَرْتَابَ
ٱلَّذِينَ أُوتُوا۟ ٱلْكِتَٰبَ وَٱلْمُؤْمِنُونَ ۙ وَلِيَقُولَ ٱلَّذِينَ فِي قُلُوبِهِم مَّرَضٌ
وَٱلْكَٰفِرُونَ مَاذَآ أَرَادَ ٱللَّهُ بِهَٰذَا مَثَلًا ۚ كَذَٰلِكَ يُضِلُّ ٱللَّهُ مَن يَشَآءُ
وَيَهْدِي مَن يَشَآءُ ۚ وَمَا يَعْلَمُ جُنُودَ رَبِّكَ إِلَّا هُوَ ۚ وَمَا هِيَ إِلَّا ذِكْرَىٰ
لِلْبَشَرِ ﴿٣١﴾ كَلَّا وَٱلْقَمَرِ ﴿٣٢﴾ وَٱلَّيْلِ إِذْ أَدْبَرَ ﴿٣٣﴾ وَٱلصُّبْحِ إِذَآ أَسْفَرَ ﴿٣٤﴾ إِنَّهَا
لَإِحْدَى ٱلْكُبَرِ ﴿٣٥﴾ نَذِيرًا لِّلْبَشَرِ ﴿٣٦﴾ لِمَن شَآءَ مِنكُمْ أَن يَتَقَدَّمَ أَوْ يَتَأَخَّرَ
﴿٣٧﴾ كُلُّ نَفْسٍۭ بِمَا كَسَبَتْ رَهِينَةٌ ﴿٣٨﴾ إِلَّآ أَصْحَٰبَ ٱلْيَمِينِ ﴿٣٩﴾ فِي جَنَّٰتٍ
يَتَسَآءَلُونَ ﴿٤٠﴾ عَنِ ٱلْمُجْرِمِينَ ﴿٤١﴾ مَا سَلَكَكُمْ فِي سَقَرَ ﴿٤٢﴾ قَالُوا۟ لَمْ نَكُ
مِنَ ٱلْمُصَلِّينَ ﴿٤٣﴾ وَلَمْ نَكُ نُطْعِمُ ٱلْمِسْكِينَ ﴿٤٤﴾ وَكُنَّا نَخُوضُ مَعَ
ٱلْخَآئِضِينَ ﴿٤٥﴾ وَكُنَّا نُكَذِّبُ بِيَوْمِ ٱلدِّينِ ﴿٤٦﴾ حَتَّىٰٓ أَتَىٰنَا ٱلْيَقِينُ ﴿٤٧﴾



(19) Don haka an tsine masa, an azabtar da shi, ta
yaya ya yi wannan qaddarawar. (20) Sannan aka
kuma tsine masa, aka qara masa azaba, t ya ya
ya yi wannan qaddarawar? (21) Sannan ya sake
tunani da nutsuwa a cikin abin da yake faxa.
(22) Sannan ya vata rai, ya xaure fuskarsa yayin
da bai samu abin da zai soki Alqur'ani da shi ba.
(23) Sannan ya bada baya ga barin yin imani,
kuma ya yi girman kai ga bin Annabi (S.A.W).
(24) Sai ya ce: "Wannan abin da Muhammad ya
zo da shi ba maganar Allah ba ce, kawai sihiri ne
yake rawaito shi daga waninsa. (25) Wannan ba
maganar Allah ba ce, maganar mutum ce kawai.
(26) Da sannu zan shigar da wannan kafiri wani
gida daga cikin gidajen wuta, ita ce wutar saqara,
ya shiga ya sha zafinta. (27) Ya kai Muhammad,
mai ya sanar da kai wutar saqara?! (28) Bata
barin abin da ake azabtawa da ita, face sai ta
gama da shi, sannan ya dawo kamar yadda yake
a da, sai kuma ta dawo kansa, haka za a yi ta
yi. (29) Mai tsananin quna ce da canza fatar jiki.
(30) A kanta akwai Mala'iku guda goma sha tara,
su ne masu gadinta. (31) Bamu sanya masu kula
da wuta ba sai Mala'iku, mutum ba zai iya da su
ba, don haka Abu Jahlin ya yi qarya lokacin da
ya yi da'awar cewa, shi da mutanensa zasu iya
gamawa da su, sannan su fito daga wuta. Kuma
bamu sanya su a wannan adadi ba (wato sha tara)
face sai don jarrabawa ga kafirai, don su faxi
abin da suka faxa, sai a ninka musu azaba, kuma
don Yahudawa waxanda aka ba su Attaura su
sakankance, haka ma Nasara waxanda aka bawa
Injila su ma su sakankance, saboda Alqur'ani
ya sauka yana mai gasgata abin da yake cikin
littafansu, Muminai kuma su qara imani, yayin
da Ahlul-kitabi suka dace da su, kuma Yahudawa da Nasara da Muminai ba zasu yi shakka ba. Kuma waxanda
suke kai-kawo a cikin imani da kafirai su kuma su ce: "Me Allah yake nufi da wannan adadin mai ban mamaki"!.
To kamar yadda wanda yake inkarin wannan adadi ya vace, wanda kuma ya gasgata da shi ya shiriya, to haka
Allah yake vatar da wanda ya ga damar vatar da shi, ya shiryar da wanda ya ga damar shiryar da shi. Babu wanda
ya san rundunar Ubangijinta saboda yawanta, sai Allah tsarki ya tabbata a gare shi. Don haka Abu Jahlin wanda
yake cewa: "Muhammad ba shi da mataimaka sai guda goma sha tara" ya san haka, don yana faxa ne don raini
da qaryatawa. Wuta kuma ba komai ba ce face tunatarwa ga mutane waxanda suka san girman Allah, tsarki ya
tabbata a gare shi. (32) Maganar ba kamar yadda wani daga cikin mushirikai yake rayawa ba ne, cewa shi zai
isarwa abokansa masu tsaron Jahannama, sai kawar da su daga kanta. Allah yana rantsuwa da wata ba haka
lamarin yake ba. (33) Yana rantsuwa da dare yayin da ya bada baya. (34) Kuma ya rantsuwa da asubahi yayi da ta
fara haskawa. (35) Tabbas wutar Jahannama tana xaya daga cikin manyan-manyan masifu masu girma. (36) Wajen
razanarwa da tsoratarwa ga mutane. (37) Wanda ya ga dama daga cikinku - Ya ku mutane – ya yi gaba da aikata
imani da ayyuka nagari, ko kuma ya yi baya ta hanyar aikata kafirci da savon Allah. (38) Kowace rai za a kamata
ne da abin da ta aikata, kodai ayyukanta su halakar da ita, ko kuma su kuvutar da ita daga halaka. (39) Amma
banda Muminai su baza a kama su da zunubansu ba, za a yafe musu saboda abin da suke da shi na ayyuka nagari.
(40) Kuma su a ranar alqiyama suna cikin Aljannatai, sashinsu yana tambayar sashi. (41) Game da Kafirai, waxanda
suka halakar da kansu ta hanyar savon Allah. (42) Suna ce musu: "Me ya shigar da ku cikin wutar Jahannama?!
(43) Sai Kafirai su amsa da cewa: "Bamu kasance daga cikin masu yin sallar farilla ba a duniya".
(44) "Kuma bamu kasance muna ciyar da mabuqaci daga dukiyar da Allah ya bamu ba".
(45) "Kuma mun kasance tare da mutanen banza, duk inda suka kasance muna biye da su, muna tattaunawa da
waxanda suka vace halakakku". (46) "Kuma mun kasance muna qaryata wa da ranar sakamako".
(47) "Muka ci gaba da qaryatawa har mutuwa ta zo mana, ta shiga tsakaninmu da tuba ga Allah".

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:** 1 - Haxarin girman kai, ta yadda ya hana Walid Bin Mugira yin imani bayan ya gane gaskiya. 2 - Mutum abin tambaya ne akan ayyukansa a duniya da lahira. 3 - Rashin ciyar da mabuqaci xaya ne daga cikin dalilai masu shigar da mutum cikin wuta.

فَمَا تَنفَعُهُمْ شَفَٰعَةُ ٱلشَّٰفِعِينَ ﴿٤٨﴾ فَمَا لَهُمْ عَنِ ٱلتَّذْكِرَةِ مُعْرِضِينَ
﴿٤٩﴾ كَأَنَّهُمْ حُمُرٌ مُّسْتَنفِرَةٌ ﴿٥٠﴾ فَرَّتْ مِن قَسْوَرَةٍۭ ﴿٥١﴾ بَلْ يُرِيدُ
كُلُّ ٱمْرِئٍ مِّنْهُمْ أَن يُؤْتَىٰ صُحُفًا مُّنَشَّرَةً ﴿٥٢﴾ كَلَّا ۖ بَل لَّا يَخَافُونَ
ٱلْءَاخِرَةَ ﴿٥٣﴾ كَلَّآ إِنَّهُۥ تَذْكِرَةٌ ﴿٥٤﴾ فَمَن شَآءَ ذَكَرَهُۥ ﴿٥٥﴾ وَمَا يَذْكُرُونَ
إِلَّآ أَن يَشَآءَ ٱللَّهُ ۚ هُوَ أَهْلُ ٱلتَّقْوَىٰ وَأَهْلُ ٱلْمَغْفِرَةِ ﴿٥٦﴾

## سُورَةُ القِيَامَةِ

ترتيبها ٧٥ — آياتها ٤٠

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

لَآ أُقْسِمُ بِيَوْمِ ٱلْقِيَٰمَةِ ﴿١﴾ وَلَآ أُقْسِمُ بِٱلنَّفْسِ ٱللَّوَّامَةِ ﴿٢﴾ أَيَحْسَبُ
ٱلْإِنسَٰنُ أَلَّن نَّجْمَعَ عِظَامَهُۥ ﴿٣﴾ بَلَىٰ قَٰدِرِينَ عَلَىٰٓ أَن نُّسَوِّىَ بَنَانَهُۥ ﴿٤﴾ بَلْ
يُرِيدُ ٱلْإِنسَٰنُ لِيَفْجُرَ أَمَامَهُۥ ﴿٥﴾ يَسْـَٔلُ أَيَّانَ يَوْمُ ٱلْقِيَٰمَةِ ﴿٦﴾ فَإِذَا بَرِقَ
ٱلْبَصَرُ ﴿٧﴾ وَخَسَفَ ٱلْقَمَرُ ﴿٨﴾ وَجُمِعَ ٱلشَّمْسُ وَٱلْقَمَرُ ﴿٩﴾ يَقُولُ ٱلْإِنسَٰنُ
يَوْمَئِذٍ أَيْنَ ٱلْمَفَرُّ ﴿١٠﴾ كَلَّا لَا وَزَرَ ﴿١١﴾ إِلَىٰ رَبِّكَ يَوْمَئِذٍ ٱلْمُسْتَقَرُّ ﴿١٢﴾ يُنَبَّؤُا۟
ٱلْإِنسَٰنُ يَوْمَئِذٍۭ بِمَا قَدَّمَ وَأَخَّرَ ﴿١٣﴾ بَلِ ٱلْإِنسَٰنُ عَلَىٰ نَفْسِهِۦ بَصِيرَةٌ ﴿١٤﴾
وَلَوْ أَلْقَىٰ مَعَاذِيرَهُۥ ﴿١٥﴾ لَا تُحَرِّكْ بِهِۦ لِسَانَكَ لِتَعْجَلَ بِهِۦٓ ﴿١٦﴾ إِنَّ عَلَيْنَا
جَمْعَهُۥ وَقُرْءَانَهُۥ ﴿١٧﴾ فَإِذَا قَرَأْنَٰهُ فَٱتَّبِعْ قُرْءَانَهُۥ ﴿١٨﴾ ثُمَّ إِنَّ عَلَيْنَا بَيَانَهُۥ ﴿١٩﴾

نصف الحزب ٥٨



(48) **Kuma ranar alqiyama ceton masu ceto ba zai yi musu amfani ba, daga cikin Mala'iku da Annabawa, da mutane nagari, domin yana daga cikin sharaxin karvar ceto yadda da wanda za a ceta. (49) Mene ne ya sanya waxannan mushirikai suke bujirewa Alqur'ani. (50) Wajen bijirewarsu ga Alqur'ani ka ce jakunan daji ne masu tsananin gudu. (51) Waxanda suka gujewa zaki saboda tsabar tsoronsa. (52) Kawai dai kowanne daga cikin waxannan mushirikai so yake ya zama da akwai wani littafi kusa da shi, da zai faxa masa cewa Muhammad Manzon Allah ne, kuma ba wai don qarancin hujjoji ko rauninsu ba, kawai taurin kai ne da kuma girman kai. (53) Lamarin ba haka yake ba, abin da ya sa suka ci gaba a cikin vatansu shi ne, su basu yi imani da azabar lahira ba ne, don haka suka zauna a cikin kafircinsu. (54) Ku Saurara, Haqiqa wanna Alqur'ani wa'azi ne da tunatarwa. (55) Wanda ya ga damar ya karanta Alqur'ani ya wa'azantu da shi, to ya karanta ya wa'azantu da shi xin. (56) Amma fa ba kowa yake wa'azantuwa ba sai wanda Allah ya ga dama ya wa'azantu. Allah shi ne wanda ya fi cancanta a ji tsoronsa, ta hanyar kamanta umarninsa, da nisantar abubuwan da ya hana, kuma shi ne wanda ya fi cancanta ya gafarta zunuban bayinsa idan suka tuba zuwa gare shi.**

# Suratul Qiyama

An Saukar Da Ita A Makkah

**Daga Manufofin Surar: Bayyanar da ikon Allah, wurin tattara halittar mutum da qara tayar da shi bayan ya mutu.**

**Tafsir: (1) Allah ya rantse da ranar tashin alqiyama, ranar da mutane zasu tashi gaban Allah Ubangijin talikai. (2) Kuma ya rantse da rai ta gari, wadda take zargin ma'abocinta a kan gazawa wajen aikata ayyuka nagari, da aikata munanan ayyuka. Allah ya rantse da waxannan lamura guda biyu cewa wallahi sai ya tashi mutane bayan mutuwarsu domin yi musu hisabi da sakamako. (3) Shin yanzu mutum yana zaton ba zamu haxa qasusuwansa bayan mutuwarsa ba, don tashin sa?! (4) Tabbas zamu iya, zamu iya haxa su, tare da dawo da masa da 'yan 'yatsunsa a cikin halitta daidaitacciya, kamar yadda take a da. (5) Kawai dai! mutum yana so ya ci gaba da yin inkarin tashin alqiyama ne domin ya ci gaba da aikata fajircinsa, a nan gaba ba tare da wani abin da zai tsoratar da shi ba. (6) Yana tambaya yana mai nuna tashin alqiyama ba zai yiwu ba, yana cewa: "yaushe tashin alqiyamar zai faru?! (7) To yayin da gani ya ruxe ya firgita, a lokacin da ya ga abin da yake qaryawa. (8) Kuma hasken wata ya tafi. (9) Kuma aka haxa gangar jikin rana da wata a wuri xaya. (10) A wannan rana mutum fajiri zai ce: ina wajen gudu?!. (11) Babu wurin gudu a wannan rana, kuma babu wurin tsira da fajiri zai fake a ciki, kuma babu wata makama da zai kama. (12) Zuwa ga Ubangijinka - Ya kai wannan Manzo - a wannan ranar makoma take kaxai, domin yin hisabi da kuma sakayya. (13) A wannan rana za a bawa mutum labarin abin da ya gabatar na ayyuka, da waxanda ya yi su daga baya. (14) Kai! mutum zai yi wa kansa shaida a kan kansa, ta yadda gavvansa zasu shaida da abin da ya aikata na laifi. (15) Koda kuwa shi ya zo da wasu dalilai nasa, da yake kansa da su, cewa shi bai aikata wani mummunan aiki ba, hakan ba zai amfane shi ba. (16) Ya kai wannan Manzo, kada ka riqa motsa harshenka, kana mai yin gaggawar koyon Alqur'ani don kada ya kuvuce maka.**

**(17) Haqiqa mu aikin mu ne mu haxa maka shi a cikin qirjinka, kuma mu tabbatar da karatunsa a kan harshenka.**

**(18) Idan Mala'ika jibrilu ya gama karatunsa a gare ka, to ka yi shiru ka saurari karatunsa.**

**(19) Sannan fassara shi gare ka shi ma yana kanmu.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa: 1 - Abin da bawa yake so yana bin bayan abin da Allah yake so ne. 2 - Kwaxayin Manzon Allah (S.A.W) wurin kiyaye wahayin Alqur'ani, da kuma bayanin irin yadda Allah ya xau nauyin tattara masa shi a qirjinsa da kiyaye shi gaba xaya, ba zai manta komai a cikinsa ba.**

كَلَّا بَلْ تُحِبُّونَ ٱلْعَاجِلَةَ ﴿٢٠﴾ وَتَذَرُونَ ٱلْـَٔاخِرَةَ ﴿٢١﴾ وُجُوهٌ يَوْمَئِذٍ نَّاضِرَةٌ
﴿٢٢﴾ إِلَىٰ رَبِّهَا نَاظِرَةٌ ﴿٢٣﴾ وَوُجُوهٌ يَوْمَئِذٍۭ بَاسِرَةٌ ﴿٢٤﴾ تَظُنُّ أَن يُفْعَلَ بِهَا
فَاقِرَةٌ ﴿٢٥﴾ كَلَّآ إِذَا بَلَغَتِ ٱلتَّرَاقِىَ ﴿٢٦﴾ وَقِيلَ مَنْ ۜ رَاقٍ ﴿٢٧﴾ وَظَنَّ أَنَّهُ ٱلْفِرَاقُ سكتة لطيفة على النون
﴿٢٨﴾ وَٱلْتَفَّتِ ٱلسَّاقُ بِٱلسَّاقِ ﴿٢٩﴾ إِلَىٰ رَبِّكَ يَوْمَئِذٍ ٱلْمَسَاقُ ﴿٣٠﴾ فَلَا
صَدَّقَ وَلَا صَلَّىٰ ﴿٣١﴾ وَلَٰكِن كَذَّبَ وَتَوَلَّىٰ ﴿٣٢﴾ ثُمَّ ذَهَبَ إِلَىٰٓ أَهْلِهِۦ يَتَمَطَّىٰٓ
﴿٣٣﴾ أَوْلَىٰ لَكَ فَأَوْلَىٰ ﴿٣٤﴾ ثُمَّ أَوْلَىٰ لَكَ فَأَوْلَىٰٓ ﴿٣٥﴾ أَيَحْسَبُ ٱلْإِنسَٰنُ
أَن يُتْرَكَ سُدًى ﴿٣٦﴾ أَلَمْ يَكُ نُطْفَةً مِّن مَّنِىٍّ يُمْنَىٰ ﴿٣٧﴾ ثُمَّ كَانَ
عَلَقَةً فَخَلَقَ فَسَوَّىٰ ﴿٣٨﴾ فَجَعَلَ مِنْهُ ٱلزَّوْجَيْنِ ٱلذَّكَرَ
وَٱلْأُنثَىٰٓ ﴿٣٩﴾ أَلَيْسَ ذَٰلِكَ بِقَٰدِرٍ عَلَىٰٓ أَن يُحْـِۧىَ ٱلْمَوْتَىٰ ﴿٤٠﴾

آياتها ٣١ — سُورَةُ الإِنسَانِ — ترتيبها ٧٦

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

هَلْ أَتَىٰ عَلَى ٱلْإِنسَٰنِ حِينٌ مِّنَ ٱلدَّهْرِ لَمْ يَكُن شَيْـًٔا مَّذْكُورًا ﴿١﴾ إِنَّا خَلَقْنَا
ٱلْإِنسَٰنَ مِن نُّطْفَةٍ أَمْشَاجٍ نَّبْتَلِيهِ فَجَعَلْنَٰهُ سَمِيعًۢا بَصِيرًا ﴿٢﴾ إِنَّا
هَدَيْنَٰهُ ٱلسَّبِيلَ إِمَّا شَاكِرًا وَإِمَّا كَفُورًا ﴿٣﴾ إِنَّآ أَعْتَدْنَا لِلْكَٰفِرِينَ سَلَٰسِلَا۟
وَأَغْلَٰلًا وَسَعِيرًا ﴿٤﴾ إِنَّ ٱلْأَبْرَارَ يَشْرَبُونَ مِن كَأْسٍ كَانَ مِزَاجُهَا كَافُورًا ﴿٥﴾



**(20) Ba haka ba ne, yadda kuka yi da'awar rashin yiwuwar tashin alqiyama, ku kun san wanda yake da ikon halittarku tun farko, ba zai gaza raya ku ba bayan mutuwarku, kawai abin da ya sa kuke qaryata tashin alqiyama shi ne, son da kuke yi wa rayuwar duniya mai saurin qarewa. (21) Da kuma barinku da rayuwar lahira, wadda hanyarta ita ce ku tsaya da abin da Allah ya umarce ku na yin xa'a, da kuma abubuwan da ya hana ku na haramun. (22) Fuskokin masu imani da arziki a wannan rana suna cike da haske da kwarjini.**
**(23) Suna masu kallon Ubangijinsu, kuma suna jin daxi da hakan. (24) Fuskokin ma'abota kafirai da tavewa a wannan rana suna xaure murtuk, babu alamun farin ciki a tare da su. (25) Sun tabbata azaba mai girma zata afka musu, da azaba mai raxaxi. (26) Lamarin ba kamar yadda mushirikai suke tunani ba ne, cewa idan sun mutu ba za a azabtar da su ba. Idan ran xayansu ya zo saman qirjinsa. (27) Sashen mutane ya cewa sashe: "Wane ne zai yi wa wannan magani wataqila ya samu waraka?!" (28) A lokacin wanda yake cikin magagin mutuwa ya tabbatar zai bar duniya ne ta hanyar mutuwa. (29) Wahalhalu da tsanani suka haxu a qarshen rayuwar duniya da farkon lahira.**
**(30) Idan haka ta faru, to za a kora mamaci zuwa ga Ubangijinsa. (31) Kafiri bai gasgata abin da Manzonsa ya zo da shi ba, kuma bai yi sallah ga Allah (S.W.T) ba. (32) Kawai dai ya qaryata abin da Manzonsa ya zo da shi, ya bijire masa. (33) Sannan wannan kafiri ya tafi wurin iyalansa yana mai yin fariya cikin tafiyarsa saboda girman kai. (34) Don haka sai Allah tsoratar da kafiri cewa, azabarsa ta tunkaro shi, da yi kusa da shi. (35) Sannan sai Allah ya sake maimaita wannan jimlar domin qarfafa magana, ya ce (Halaka ta tabbata a gare ka, kuma halaka da tabbata a gare ka). (36) Shin yanzu mutum yana zaton Allah zai bar shi kara zube ne, ba tare da ya xora masa wani nauyi na shari'a ba?! (37) Shin wannan mutum a wani lokaci can baya bai kasance xigon maniyi ba ne, wanda ake zuba shi a cikin mahaifa ba?! (38) Sannan bayan haka ya kasance wani yanki na daskararren jini, sannan Allah ya halicce shi, kuma ya sanya shi cikakkiyar halitta daidaitacciya. (39) Kuma ya sanya shi jinsi guda biyu, namiji, da mace?! (40) Shin yanzu wanda ya halicci mutum daga xigon maniyi, sannan gudan jini, ba mai iko ba ne akan raya matattu, domin yi musu hisabi da sakayya ba a wani karo daban?! Tabbas haka ne, shi mai iko ne a kan aiwatar da hakan.**

# Suratul Insaan

An Saukar Da Ita A Makkah

**Daga Manufofin Surar:** **Tunatar da mutum asalinsa, da hikimar halittarsa, da makomarsa a duniya da lahira, da bayyana ni'imar Aljannah, domin tabbatar da Muminai, da kuma kira ga kafirai.**

**Tafsir:** **(1) Haqiqa zamani mai tsawo ya wuce ga mutum, lokacin babu shi, kuma babu ambatonsa.**
**(2) Haqiqa mun halicci mutum daga xigon maniyi, wanda ya cuxanya da tsakanin ruwan namiji da ruwan mace, kuma muna jarrabarsa da nauyin da muke xora masa na shari'a, don haka sai muka sanya shi ya zama mai ji kuma mai gani, domin ya iya sauke nauyin da muka xora masa na shari'a. (3) Haqiqa mun bayyana masa hanyar shiriya bisa harshen Manzannin mu, sai hanyar vata ta bayyana gare shi, don haka bayan wannan bayanin, kodai ya shiriya zuwa tafarki madaidaci, ya zama bawa mumini mai godiya ga Allah, ko kuma ya vace, ya zama bawa kafiri mai inkarin ayoyin Allah. Yayin da Allah ya bayyana akwai shiryayye da vatacce, sai kuma ya bayyana sakamakon kowannensu, ya ce: (4) Haqiqa mun tanadar wa masu kafircewa Allah da Manzanninsa sarqoqi waxanda za a ja su da su zuwa wuta, da marurruka da za a xaure su da su, da wuta mai ci ganga-ganga. (5) Haqiqa Muminai masu biyayya ga Allah, ranar alqiyama zasu sha daga wani kofin giya cikakke, wanda aka haxa da kafur, saboda daxin qanshinsa.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:** 1 - **Haxarin son duniya da bijirewa lahira.**
2 - **Tabbatar da cewa xan Adam yana da zavi, kuma wannan yana cikin girmamawar Allah ga xan Adam.**
3 - **Duba zuwa ga fuskar Allah mai girma, yana cikin manyan ni'imomi.**

عَيْنًا يَشْرَبُ بِهَا عِبَادُ ٱللَّهِ يُفَجِّرُونَهَا تَفْجِيرًا ٦ يُوفُونَ بِٱلنَّذْرِ وَيَخَافُونَ
يَوْمًا كَانَ شَرُّهُۥ مُسْتَطِيرًا ٧ وَيُطْعِمُونَ ٱلطَّعَامَ عَلَىٰ حُبِّهِۦ مِسْكِينًا
وَيَتِيمًا وَأَسِيرًا ٨ إِنَّمَا نُطْعِمُكُمْ لِوَجْهِ ٱللَّهِ لَا نُرِيدُ مِنكُمْ جَزَآءً وَلَا شُكُورًا
٩ إِنَّا نَخَافُ مِن رَّبِّنَا يَوْمًا عَبُوسًا قَمْطَرِيرًا ١٠ فَوَقَىٰهُمُ ٱللَّهُ شَرَّ ذَٰلِكَ
ٱلْيَوْمِ وَلَقَّىٰهُمْ نَضْرَةً وَسُرُورًا ١١ وَجَزَىٰهُم بِمَا صَبَرُوا۟ جَنَّةً وَحَرِيرًا ١٢
مُّتَّكِـِٔينَ فِيهَا عَلَى ٱلْأَرَآئِكِ ۖ لَا يَرَوْنَ فِيهَا شَمْسًا وَلَا زَمْهَرِيرًا ١٣
وَدَانِيَةً عَلَيْهِمْ ظِلَـٰلُهَا وَذُلِّلَتْ قُطُوفُهَا تَذْلِيلًا ١٤ وَيُطَافُ عَلَيْهِم بِـَٔانِيَةٍ
مِّن فِضَّةٍ وَأَكْوَابٍ كَانَتْ قَوَارِيرَا۠ ١٥ قَوَارِيرَا۟ مِن فِضَّةٍ قَدَّرُوهَا تَقْدِيرًا ١٦
وَيُسْقَوْنَ فِيهَا كَأْسًا كَانَ مِزَاجُهَا زَنجَبِيلًا ١٧ عَيْنًا فِيهَا تُسَمَّىٰ سَلْسَبِيلًا
ثلاثة أرباع الحزب ٥٨ ١٨ ۞ وَيَطُوفُ عَلَيْهِمْ وِلْدَٰنٌ مُّخَلَّدُونَ إِذَا رَأَيْتَهُمْ حَسِبْتَهُمْ لُؤْلُؤًا مَّنثُورًا
١٩ وَإِذَا رَأَيْتَ ثَمَّ رَأَيْتَ نَعِيمًا وَمُلْكًا كَبِيرًا ٢٠ عَـٰلِيَهُمْ ثِيَابُ سُندُسٍ
خُضْرٌ وَإِسْتَبْرَقٌ ۖ وَحُلُّوٓا۟ أَسَاوِرَ مِن فِضَّةٍ وَسَقَىٰهُمْ رَبُّهُمْ شَرَابًا
طَهُورًا ٢١ إِنَّ هَـٰذَا كَانَ لَكُمْ جَزَآءً وَكَانَ سَعْيُكُم مَّشْكُورًا ٢٢ إِنَّا
نَحْنُ نَزَّلْنَا عَلَيْكَ ٱلْقُرْءَانَ تَنزِيلًا ٢٣ فَٱصْبِرْ لِحُكْمِ رَبِّكَ وَلَا تُطِعْ
مِنْهُمْ ءَاثِمًا أَوْ كَفُورًا ٢٤ وَٱذْكُرِ ٱسْمَ رَبِّكَ بُكْرَةً وَأَصِيلًا ٢٥



(6) Wannan abin shan da aka tanadar wa masu xa'a ga Allah, yana kwaranyowa daga wani idon ruwa marar wahalar xiba, kuma mai yawa baya qafewa, bayin Allah suna qoshi da shi, suna jan shi, suna gudanar da shi zuwa inda suka ga dama. (7) Siffofin bayin da suke shan wannan ruwan su ne, suna cika alqawarin abin da suka xaukar wa kansu na xa'ar Allah, kuma suna tsoron wani yini da sharrinsa yake barbazuwa, shi ne yinin ranar alqiyama. (8) Kuma suna ciyar da abinci tare da kasancewarsu suna son sa don buqatarsu da sha'awarsa gare shi. Suna ciyar da shi ga mabuqata, da marayu, da ribatattun yaqi. (9) Suna voyewa a cikin ransu, cewa suna ciyar da su ne domin neman yardar Allah, basa neman wani sakamako daga wurinsu, ko wani yabo a kan ciyar da su da suke yi. (10) Haqiqa muna jin tsoron wata rana daga Ubangijinmu, wadda fuskar shaqiyyai take xaurewa, saboda tsananin ranar da ban-tsoronta. (11) Sai Allah ya kare su da falalarsa daga sharrin wannan rana, ya ba su kwarjini da haske a fuskokinsu, domin girmamawa gare su, da shigar musu da farin ciki a zukatansu. (12) Kuma Allah ya ba su ladan Aljannah, da alharirin da suke sakawa, saboda haqurinsu a kan xa'ar Allah, da haqurinsu a kan abubuwan da Allah ya qaddara, da haqurinsu a kan barin savon Allah. (13) Suna kishingixe a cikin wannan Aljannah, a kan gadaje masu ado, kuma a cikinta basa ganin ranar da haskenta zai cutar da su, ko sanyi mai tsanani, suna cikin inuwa dauwamammiya, wadda babu zafi ko sanyi a cikinta. (14) Inuwar Aljannar tana kusa da su, kuma an hore 'ya'yan itacenta ga mai buqata, sai ya tsinka a cikin sauqi, ta yadda wanda yake kwance, da wanda yake zaune, da wanda yake tsaye, duk zasu iya tsinka.

(15) Kuma masu hidima suna kewaya su da mazubai na azurfa, da kofunanta, waxanda launinsu yake garai-garai, yayin da suke so su sha wanin abin sha. (16) Kai ka ce kwalba ce wajen garai-garai xin launita, sai dai azurfa ce ba kwalba ba, kuma an tanade ta yadda suke so, babu daxi babu ragi. (17) Ana shayar da waxannan masu girman abin sha na giya, wadda aka haxa shi da citta. (18) Kuma suna sha daga wani idon ruwa a cikin gidan Aljannah ana kiransa Salsabil. (19) Kuma wasu yara waxanda suke kan samartakar su suna kewaya su a cikin gidan Aljannah, idan ka gan su sai ka yi zaton su lu'u lu'u ne wanda aka watsa shi, saboda kwarjininsu da hasken fuskarsu da kyawunsu da yawansu da rarrabuwarsu. (20) Kuma idan ka kalli abin da yake can a cikin Aljannah, zaka ga ni'imar da ba zata siffatu ba, da mulkin da ba mulkin da ya kai shi.

(21) Suna sanye da korayen tufafi na alfahari, na alhariri marar kauri, da mai kauri a jikinsu, kuma an sanya musu awarwaro na azurfa. Kuma Ubangijinsu ya shayar da su abin sha wanda babu abin da ya vata shi.

(22) Kuma ana ce musu – don girmama su - : "Wannan ni'imar da aka ba ku, sakamako ce na ayyukanku na qwarai, kuma aikinku karvavve ni a wurin Allah".

(23) Ya kai wannan Manzo, Haqiqa mu ne muka saukar maka da Alqur'ani a rarrabe, ba mu saukar maka da shi a dunqule ba. (24) Don haka ka yi haquri dangane da abin da Ubangijinka ya hukunta a shari'ance ko kuma a rayuwa, kada ka bi mai savo a cikin abin da yake kira na savo, ko kuma kafiri a cikin abin da yake kira na kafirci.

(25) Kuma ka ambaci Ubangijinka, ta hanyar yin sallar asuba a farkon yini, da kuma sallar azzahar da la'asar a qarshen yini.

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

1 - Cika bakance da ciyar da mabuqaci, da tsarkake niyya a wurin aiki, da tsoron Allah, sabubba ne na kuvuta daga shiga wuta, da kuma shiga Aljannah. 2 - Idan wannan ne siffar yaran da suke yi musu hidima a cikin Aljannah, wajen kyau, to yaya 'yan Aljannar suke?!

وَمِنَ ٱلَّيۡلِ فَٱسۡجُدۡ لَهُۥ وَسَبِّحۡهُ لَيۡلٗا طَوِيلًا ٢٦ إِنَّ هَٰٓؤُلَآءِ
يُحِبُّونَ ٱلۡعَاجِلَةَ وَيَذَرُونَ وَرَآءَهُمۡ يَوۡمٗا ثَقِيلٗا ٢٧ نَّحۡنُ خَلَقۡنَٰهُمۡ
وَشَدَدۡنَآ أَسۡرَهُمۡۖ وَإِذَا شِئۡنَا بَدَّلۡنَآ أَمۡثَٰلَهُمۡ تَبۡدِيلًا ٢٨ إِنَّ
هَٰذِهِۦ تَذۡكِرَةٞۖ فَمَن شَآءَ ٱتَّخَذَ إِلَىٰ رَبِّهِۦ سَبِيلٗا ٢٩ وَمَا تَشَآءُونَ
إِلَّآ أَن يَشَآءَ ٱللَّهُۚ إِنَّ ٱللَّهَ كَانَ عَلِيمًا حَكِيمٗا ٣٠ يُدۡخِلُ
مَن يَشَآءُ فِي رَحۡمَتِهِۦۚ وَٱلظَّٰلِمِينَ أَعَدَّ لَهُمۡ عَذَابًا أَلِيمَۢا ٣١

## سُورَةُ المُرۡسَلَاتِ

آياتها ٥٠ — ترتيبها ٧٧

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

وَٱلۡمُرۡسَلَٰتِ عُرۡفٗا ١ فَٱلۡعَٰصِفَٰتِ عَصۡفٗا ٢ وَٱلنَّٰشِرَٰتِ نَشۡرٗا ٣
فَٱلۡفَٰرِقَٰتِ فَرۡقٗا ٤ فَٱلۡمُلۡقِيَٰتِ ذِكۡرًا ٥ عُذۡرًا أَوۡ نُذۡرًا ٦ إِنَّمَا
تُوعَدُونَ لَوَٰقِعٞ ٧ فَإِذَا ٱلنُّجُومُ طُمِسَتۡ ٨ وَإِذَا ٱلسَّمَآءُ فُرِجَتۡ
٩ وَإِذَا ٱلۡجِبَالُ نُسِفَتۡ ١٠ وَإِذَا ٱلرُّسُلُ أُقِّتَتۡ ١١ لِأَيِّ يَوۡمٍ أُجِّلَتۡ
١٢ لِيَوۡمِ ٱلۡفَصۡلِ ١٣ وَمَآ أَدۡرَىٰكَ مَا يَوۡمُ ٱلۡفَصۡلِ ١٤ وَيۡلٞ يَوۡمَئِذٖ
لِّلۡمُكَذِّبِينَ ١٥ أَلَمۡ نُهۡلِكِ ٱلۡأَوَّلِينَ ١٦ ثُمَّ نُتۡبِعُهُمُ ٱلۡأٓخِرِينَ
١٧ كَذَٰلِكَ نَفۡعَلُ بِٱلۡمُجۡرِمِينَ ١٨ وَيۡلٞ يَوۡمَئِذٖ لِّلۡمُكَذِّبِينَ ١٩



**(26) Ka ambaci Allah ta hanyar salloli biyu na dare, sallar magariba da sallar isha'i, sannan ka yi sallar dare bayan waxannan salloli. (27) Haqiqa waxannan mushirikai suna son rayuwar duniya, kuma suna kwaxayinta, kuma suna barin ranar alqiyama a bayansu, alhali rana ce mai nauyi, saboda abin da yake cikinta na tsanani da masifu. (28) Mu ne muka halicce su, kuma muka qarfafi halittarsu ta hanyar gavvansu da sauran jikinsu, idan muka ga damar halakar da su ko mu zo da wasu makamantansu, sai mu halakar da su, mu canza su da wasun su. (29) Haqiqa wannan sura wa'azi ce da tunatarwa, don haka duk wanda ya ga damar ya riqi wata hanya wadda zata sada shi da yardar Ubangijinsa, to sai ya riqe ta. (30) Sai dai ba zaku iya riqar wata hanya da zata sadar da ku da yardar Ubagijinku ba, har sai Allah ya ga damar hakan, duk lamura suna hannunsa, Haqiqa Allah masani ne ga abin da ya dace da bayinsa, da abin da bai dace da su ba, kuma mai hikima ne cikin halittarsa da qaddarawarsa da shari'arsa. (31) Yana shigar da wanda ya so daga cikin bayinsa a cikin rahamarsa, sai ya datar da su ga imani, da aiki nagari, kuma Allah ya tanadar wa waxanda suka zalunci kansu da kafirci da savo azaba mai raxaxi a lahira, ita ce azabar wuta.**

# Suratul Mursalat

An Saukar Da Ita A Makkah

## Daga Manufofin Surar:

**Tabbatar da tashin alqiyama, ta hanyar yin jayayya da masu qaryata afkuwarta da dalilai, da kuma biyo hakan da bayanan narkon azaba da tsoratarwa.**

## Tafsir:

**(1) Allah ya rantse da iska wadda take bin juna, tamkar gashin wuyan doki.**
**(2) Kuma ya rantse da iska mai tashi da qarfi. (3) Kuma ya rantse da iska wadda take watsa ruwan sama.**
**(4) Kuma ya rantse da Mala'iku, waxanda suke saukowa da abin da yake rabewa tsakanin qarya da gaskiya.**
**(5) Kuma ya rantse da Mala'ikun da suke saukowa da wahayi. (6) Suna saukowa da wahayi, don yankewa mutane uzuri a wajen Allah, da gargaxinsu daga azabar Allah. (7) Tabbas abin da ake alqawarta muku na tashin alqiyama da hisabi, da bada sakamako, mai faruwa ne babu makawa. (8) Idan taurari aka tafiyar da haskensu, aka shafe shi. (9) Idan sama ta kekkece, domin Mala'iku su sauko daga cikinta. (10) Kuma Idan aka tunvuke duwatsu daga gurabensu, aka dagargaza su, suka zama kamar toka. (11) Kuma idan aka haxa Manzanni a wuri guda, na xan wani lokaci iyakantacce. (12) Don wani yini mai girma, wanda aka jinkirta shi, don Manzanni su yi shaida a kan al'ummunsu. (13) Don ranar yin hukunci a tsakanin bayi, mai gaskiya ya bayyana daga marar gaskiya, kuma xan Aljannah ya bayyana daga xan wuta. (14) Ya kai wannan Manzo me ya sanar da kai ranar sakamako?!**
**(15) Halaka ce da azaba da asara a wannan rana ga masu qaryatawa, waxanda suke qaryata abin da Manzanni suka zo da shi daga wurin Allah. (16) Shin bamu halakar da al'ummun da suka gabata ba, yayin da suka qaryata Manzanninsu?! (17) Sannan muke biye bayan masu qaryatawa da waxanda suka zo daga qarshe, su ma muka halakar da su, kamar yadda muka halakar da na farkon?!. (18) To kamar yadda muka halakar da waxancan al'ummu, to haka muke halakar da masu laifi, waxanda suke qaryata abin da Annabi muhammad (S.A.W) ya zo da shi. (19) Halaka da azaba da asara a wannan rana, sun tabbata ga masu qaryata alqawarin azaba da uquba da Allah ya yi wa masu laifi.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Haxarin rataya da duniya, da mancewa da lahira. 2 - Ganin damar bawa tana bin bayan abin da Allah ya ga dama ne. 3 - Halakar da al'ummun da suka qaryata sunna ce ta Ubangiji.**

أَلَمۡ نَخۡلُقكُّم مِّن مَّآءٖ مَّهِينٖ ٢٠ فَجَعَلۡنَٰهُ فِي قَرَارٖ مَّكِينٍ ٢١ إِلَىٰ قَدَرٖ
مَّعۡلُومٖ ٢٢ فَقَدَرۡنَا فَنِعۡمَ ٱلۡقَٰدِرُونَ ٢٣ وَيۡلٞ يَوۡمَئِذٖ لِّلۡمُكَذِّبِينَ ٢٤
أَلَمۡ نَجۡعَلِ ٱلۡأَرۡضَ كِفَاتًا ٢٥ أَحۡيَآءٗ وَأَمۡوَٰتٗا ٢٦ وَجَعَلۡنَا فِيهَا رَوَٰسِيَ
شَٰمِخَٰتٖ وَأَسۡقَيۡنَٰكُم مَّآءٗ فُرَاتٗا ٢٧ وَيۡلٞ يَوۡمَئِذٖ لِّلۡمُكَذِّبِينَ ٢٨
ٱنطَلِقُوٓاْ إِلَىٰ مَا كُنتُم بِهِۦ تُكَذِّبُونَ ٢٩ ٱنطَلِقُوٓاْ إِلَىٰ ظِلّٖ ذِي ثَلَٰثِ
شُعَبٖ ٣٠ لَّا ظَلِيلٖ وَلَا يُغۡنِي مِنَ ٱللَّهَبِ ٣١ إِنَّهَا تَرۡمِي بِشَرَرٖ
كَٱلۡقَصۡرِ ٣٢ كَأَنَّهُۥ جِمَٰلَتٞ صُفۡرٞ ٣٣ وَيۡلٞ يَوۡمَئِذٖ لِّلۡمُكَذِّبِينَ ٣٤
هَٰذَا يَوۡمُ لَا يَنطِقُونَ ٣٥ وَلَا يُؤۡذَنُ لَهُمۡ فَيَعۡتَذِرُونَ ٣٦ وَيۡلٞ يَوۡمَئِذٖ
لِّلۡمُكَذِّبِينَ ٣٧ هَٰذَا يَوۡمُ ٱلۡفَصۡلِۖ جَمَعۡنَٰكُمۡ وَٱلۡأَوَّلِينَ ٣٨ فَإِن كَانَ
لَكُمۡ كَيۡدٞ فَكِيدُونِ ٣٩ وَيۡلٞ يَوۡمَئِذٖ لِّلۡمُكَذِّبِينَ ٤٠ إِنَّ ٱلۡمُتَّقِينَ
فِي ظِلَٰلٖ وَعُيُونٖ ٤١ وَفَوَٰكِهَ مِمَّا يَشۡتَهُونَ ٤٢ كُلُواْ وَٱشۡرَبُواْ هَنِيٓـَٔۢا
بِمَا كُنتُمۡ تَعۡمَلُونَ ٤٣ إِنَّا كَذَٰلِكَ نَجۡزِي ٱلۡمُحۡسِنِينَ ٤٤ وَيۡلٞ
يَوۡمَئِذٖ لِّلۡمُكَذِّبِينَ ٤٥ كُلُواْ وَتَمَتَّعُواْ قَلِيلًا إِنَّكُم مُّجۡرِمُونَ ٤٦ وَيۡلٞ
يَوۡمَئِذٖ لِّلۡمُكَذِّبِينَ ٤٧ وَإِذَا قِيلَ لَهُمُ ٱرۡكَعُواْ لَا يَرۡكَعُونَ ٤٨
وَيۡلٞ يَوۡمَئِذٖ لِّلۡمُكَذِّبِينَ ٤٩ فَبِأَيِّ حَدِيثِۢ بَعۡدَهُۥ يُؤۡمِنُونَ ٥٠



**(20) Ya ku mutane, shin ba mu halicce ku daga wulaqantaccen ruwa ba, kuma xan kaxan, shi ne xigon maniyyi?!. (21) Muka sanya wannan wulaqantaccen ruwan a wani wuri tsararre, shi ne mahaifar mace. (22) Har zuwa wani lokaci sananne, shi ne lokacin goyon ciki.**
**(23) Sai muka qaddara siffar abin da za a haifa, da gwargwadonsa, da launinsa, da wanin hakan. Madalla da masu tsara hakan, mu kenan.**
**(24) Halaka da azaba da asara a wannan rana sun tabbata ga masu qaryata ikon Allah.**
**(25) Shin ba mu sanya qasa tana tattaro mutane gaba xaya ba. (26) Ta tattaro rayayyunsu ta hanyar zama a bayanta da raya ta da gine-gine, matattunsu kuma da binnewa a cikinta.**
**(27) Kuma muka sanya tabbatattun duwatsu a cikinta, da suke hana ta girgiza da motsi, masu tsawo. Kuma mun shayar da ku ruwa mai daxi – Ya ku mutane. Wanda ya halicci wannan ba zai kasa tashin ku ba, bayan kun mutu.**
**(28) Halaka da azaba da asara a wannan rana sun tabbata ga masu qaryata ni'imomin Allah.**
**(29) Za a cewa masu qaryata abin da Manzanninsu suka zo da shi: "Ku tafi – Ya ku masu qaryatawa - zuwa ga abin da kuke qaryatawa na azaba".**
**(30) Ku tafi zuwa ga wata inuwa ta hayaqin wuta, wanda ta rabu gida uku. (31) Babu sanyin inuwa a cikinta, kuma bata kare ku da harshen wuta da zafinta. (32) Tabbas wuta tana fitar da tartsatsi, kowane tartsatsi kamar girman qaton gida yake.**
**(33) Kai ka ce tartsatsin da wutar take fitarwa wasu baqaqen rakuma ne qirin, wajen girma da baqi. (34) Halaka da azaba da asara a wannan rana sun tabbata ga masu qaryata azabar Allah.**
**(35) Wannan rana ce da basa faxin komai. (36) Kuma baza a ba su izinin su gabatar da hanzari ga Ubangijinsu ba bisa Kafircinsu da miyagun ayyukansu, ballantana su gabatar masa da hanzarinsu. (37) Halaka da azaba da asara a wannan rana sun tabbata ga masu qaryata labaran wannan rana. (38) Wannan ita ce ranar yanke hukunci a tsakanin halittu, mun tara ku da al'ummun da suka gabata a fili guda xaya. (39) To idan kuna da wata dabara da zaku iya gujewa azabar Allah, to ku yi min dabarar mana. (40) Halaka da azaba da asara a wannan rana sun tabbata ga masu qaryatawa da ranar sakamako. (41) Haqiqa masu jin tsoron Ubangijinsu ta hanyar aikata umarninsa, da nisantar abubuwan da ya hana, suna cikin inuwar bishiyoyin gidan Aljannah masu ganye, da idanuwan ruwa masu daxi, masu gudana. (42) Da kayan marmari, waxanda suke sha'awar cin su. (43) Kuma za a ce musu: "Ku ci daga daxaxan abubuwa, kuma ku sha, abin sha mai daxi, babu wata damuwa a cikinsa, saboda abin da kuka kasance suna aikatawa a duniya, na daga kyawawan ayyuka". (44) Haqiqa irin wannan sakamako da muka saka muku da shi, haka muke sakawa masu kyautata ayyukansu.**
**(45) Halaka da azaba da hasara a wannan rana sun tabbata ga masu qaryata abin da Allah ya tanadar wa masu tsoronsa. (46) Za a cewa masu qaryatawa: "Ku ci, ku ji daxin duniya na xan wani lokaci kaxan a duniya, tabbas ku saboda kafircinku da Allah, da kuma qaryatawar ku ga Manzanninsa masu laifi ne".**
**(47) Halaka da azaba da asara a wannan rana sun tabbata ga masu qaryatawa da sakamakonsu ranar alqiyama.**
**(48) Kuma idan aka cewa waxannan masu qaryatawa: "Ku yi sallah saboda Allah, sai su qi yin sallar".**
**(49) Halaka da azaba da asara a wannan rana sun tabbata ga masu qaryatawa, waxanda suke qaryata abin da Manzanni suka zo da shi daga wurin Allah. (50) To idan ba su yi imani da wannan Alqur'ani ba, wanda aka saukar daga Ubangijinsu, da wace magana kuma zasu yi imani?!.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa: 1 - Kulawar da Allah yake yi wa xan Adam tun yana cikin mahaifiyarsa. 2 - Yadda qasa ta yalwaci waxanda suke raye a bayanta, da kuma waxanda suke cikinta daga matattu. 3 - Haxarin qaryatawa da ayoyin Allah, da kuma bayanan narkon azaba ga wanda ya aikata hakan.**